Zuwa wannan lokaci har ta gaji da kiran wayar Ma'eesh ta haƙura ta sallama tanajin cewa ita kaɗai ce kawai keda Jany, tayi nufin shirya tafiya don zuwa ta gano meye yake faruwa saidai tuna turakunan da rayuwarta ta tsallake har Allah ya kawota yanzu yana kashe mata gwiwa karshe ta sanar da Samha sosai ta fusata tace “idan shi bai nemeki ba Mom Jany bai kamata ke ki zubar da yanci ki nemeshi ba ai shine yake da abun nema a gurinki kinga kuwa shi nemanki ya kama" haka ta haƙura ta sallama.
Yau dake asabar ce basu da aiki suna zaune a parlour Jany ta miƙe ta fara tafiyarta sosai shekara ɗaya da rabi Batul ta dubi Samha tace “Kinsan me yake zuwa raina?" Girgiza mata kai tayi ta sauke ajiyar zuciya tace “Inason zuwa Nigeria Mahaifiyata nakeson naje na gani" jinjina kai tayi tace “Nima ina shirin yi Miki maganar kika rigani duk da cewa babu abinda na bari a TChad Inason zuwa naga kawaye da yan'uwana da suka wofintar dani kinga daganan sai muyi Nigeria yanzu mu shirya tafiya yaushe kike ganin zamu tafi?"
Murmushi tayi tace “Ƙarshen wata ko? Kinga ko 1 month sai muyi mu dawo amma ke me kika gani?" Jinjina mata tayi tace “Hakan yayi zamu tafi da yaran ne ko zamu barsu gidan raino?" Zaro idanu Batul tayi tace “Ni shegiya inji ɗan daudu ai ƙafata ƙafar Jany na bazan iya kwana batare da ita ba ke nifa yanda nakejin Jany a raina banajin kaina" dariya sukayi suka tashi suka fice suka nufi beach yauma kamar kullum a inda suka saba zama suka zauna aka kawo musu

kofin coffee kowacce na danna wayarta suna hira sama sama, sallama sukaji a bayansu abinda yasa Samha juyawa tare da kallon me sallamar wanda idanunsa ke kan Batul da ko arziƙin ta ɗago ta kalleshi bai samu ba"
Numfasawa yayi yace “Ko zan iya zama?" Jinjina masa kai Samha tayi tare da gyara masa wajen zama ya zauna yana kama hannun Jany yace “Ƴar uwar taki kurma ce halan?" Sai yanzu ta ɗago ta watsa masa wani mugun kallo tare da miƙewa taja hannun Jany suka bar gurin, ya bita da kallo cike da mamaki yace “Ni sunana Nuraddeen ana kirana da Deen ɗan Nigeria ne ni Kano shine garin iyaye na amma mazaunan Abuja ne Ni kuma ina aiki anan kuma ina kasuwanci, am ƙawarki ta daɗe tana burgeni saidai yanda naga bata bawa Kowa dama yasa nima jikina yayi sanyi duk da ƙarin abinda yasa naƙi zuwa gareku da ƙoƙon barata saboda a farko na zaci matar aure ce sai daga baya nake samun labarin bata da aure"
Zamewa yayi daga kan kujerar yace “Don Allah in da hali ki shigar da ƙoƙon barata gareta wlh ba da wasa nake ba idan ta amince ko ina iyayenta suke a duniya zan tura nawa ayi magana nidai burina ta karɓeni ta yarda da buƙatata" jinjina kai Samha tayi tace “To Deen saidai a gwada wannan kawar tawa dakon son gaibu takeyi taƙi kallon kowa bare ta bashi dama amma zanyi maka bakin ƙoƙari" godiya sosai yayi sukayi musayar number tare da bashi ta Batul sukayi sallama ya tafi itama ta tashi ta isa motarsu ta tarar da Batul ta cika ta batse tace “Tuba nake Allah ya taimakeki kinsan Allah ya karrama ɗan adam musamman wannan bawan kammalalle Ni tunda nake zuwa gurin nan bantaɓa ganin yayiwa wata mace magana ba sai yau yawanci a gefe zaki sameshi yana yan aikace aikacensa"  cikin hassala tace “to aku me magana kizo ki kaimu gida ko ki bamu mukullin mu tafi".........

*_Assalamu alaikum everyone_*

*Sunana Fauziyya Tasiu Umar (OUM HAIRAN)*

Yau muna birthday Hairan da Widad dole muyi promo 300 Nrml group VIP 600 please iya yau ne kaɗai

Kar kuyi ƙasa a gwiwa kuzo ku runguntsuma ku tattaru muji chakwalkwalin chakwakiyar nan me rikita tunani da sanya shauƙi, shin ya rayuwar zata kasance bayan kowa yayi baram baram da hanyar Allah? Akwai sauran damar tuna ko lokaci ya ƙure?

And please  adult contact ne wannan labarin don Allah in Baki iyawa ki haƙura don wlh sai na zubar da Abin a wannan book ɗin.

Via 300 Normal group VIP 600 only
9031307566 Fauziyya Tasiu Umar Opay Evidence 09031307566.

please Ku daina turamin Evidence ta wannan number 09013718241 course saƙonni suna yawa a kanta.

*In kun shirya🤗 Nima na shirya👌🏽*

*Oum Hairan*
[7/7, 4:51 PM] Oum Hairan: *SIGNED MARRIAGE*
*_(Kalma ɗaya)_*

*Oum Hairan*
*______________________________________*
Book 2 page 9-10
*______________________________________*

Dariya Samha tayi tace nidai zanga inda inda zakikai wannan kayan da kiketa tsumawa saidai ki wanke kisa masa pant, Please Teemah tunda dai kinƙi ki bada na haram aci aji daɗi a raƙashe a hole yanzu ga zancen gsky yazo Allah kar kiyi sake da damarki Wannan guy ɗin ya haɗu sosai" banza tayi da ita har sukaje gida ta shigewarta ɗakinta ta cire kayanta tayi wanka tayiwa ɗiyarta ta sanya mata kayan sanyi itama tasa domin yau alamun ya nuna dusar ƙanƙara za'a kwana zubar musu.
Room hitter ta kunna ta kulle ko ina kasancewa bata sallah taja ƴarta suka kwanta cike da kewar ɓangarorin rayuwarta kamar yanda ta saba ta ɗauki wayarta ta fara kiraye kirayen numbers cikin numbers biyar data kira ɗaya ce ta shiga ta Laminu me shayi ta daɗe tana ring ba'a ɗaga ba Saida ta kira so uku sannan aka daga tace “Assalamu Alaikum Laminu Batula ce" ajiyar zuciya ya sauke yace “Hajiya Batulu ta Manzo kwana biyu" murmushin yaƙe tayi tace “Don Allah ko zan iya magana da Innata?" “Toh Batulu Ni yanzu ina zan samu Inna Laure ai tunda kikayi aure itama ta tashi ta koma gidan benen da mijinki ya siya mata ta rangaɗa aurenta da Idi dillali ban kuma ganinta ba sai watanni biyar da suka wucce da na haɗu da ƙawarki Murjanatu nake tambayarta labarin Inna Laure take faɗamin ai tasai da gidan da mijinki ya bata ta Idi dillali Lagos yanzu haka suna can"
Tashin hankali sosai ta shiga tace “yanzu ya akayi duk haka ta faru Bansani ba Meyesa kullum wayoyinku basa shiga yanzu ina zaka nemonin Murjah?" Cewa yayi “ah ita wannan tana gidansu bata samu promotion irin naki ba duniya tayi mata attishawar tsaki tananan tana fama

da ciwon nan na zamani in ta fara gudawa har ƙofar gida" cikin tashin hankali tace “Eh Murjanatun? Yaushe ta gamu da wannan ciwon Innanillahi wa innah ilaihirraji'un don Allah Laminu ka haɗani da ita ka turomin account ɗinka xansa maka kuɗi kaima ka ƙara jari"

************

Sosai ya rinƙa mata Godiya ya kashe wayar ya kalli mutanen kusa dashi yace “Waye zai iya kaiwa Murja Waya zasuyi magana da Batulu" Isah ɗan garuwa ne yace “Ah zan iya amma nawa zaka bani?" Cikin masifa yace “Kaidai kwai maye to kaje ka kai mana sai mu tura acct ɗin muga nawa za'a Turo mana" karɓa yayi ya tafi ya kaiwa Murja tana zaune a zauren gidansu duk ta kwarjale ga ciwo babu kuɗin shan magani, daga bakin ƙofa yace mata “Batula ce tace a kawo Miki waya" cike da zumuɗi ta karɓi wayar, tana karɓa kuwa tana kira tace “Batulu kin samu duniya kin barmu a wahala ko nemanmu bakyayi" numfasawa tayi tace “ta ina zan nemeki Janah sama da shekara guda nake kiranki wayarki bata shiga idan na kira ta Laminu me shayi shima bata tafiya daƙyar yau Allah ya bani Sa'a na sameshi Janah meye yake faruwa ne ance Inna ta tabar Kano ta koma Lagos ina zan samu lambar da zan sameta?"
Girgiza kai tayi cike da tausayawa kai tace “Ki bari kawai Batulu babu yanda bamuyi ba nida Mamanmu kan Inna karta yarda da zugar mugun mutumin nan ta siyar da gidanta amma ta fitittike taci mutumcinmu har tana cewa baƙin ciki mukeyi mata likkafarta zata ƙara ci gaba zata tashi daga cikin talakawa taka koma cikin danginta masu kuɗi  haka munaji muna gani ta siyar da gidan da Yake mallakinki wanda Ma'eesh ya baki matsayin Fansar budurcinki Naira Miliyan ɗari uku da hamsin, wlh Batul ko la'ada Duk kyauta ta Inna Laure Idi dillali bai barta ta bamu ba cikin dare ya kawo mota suka ɗebi tsirarin kayansu tunda dama furniture duk a suna cikin ciniki, suka tafi suka bar unguwar nan babu sallama yanzu haka dai zancen da nake Miki wata rana na haɗu da Inna ga tsohon ciki a jikinta ga bara tanayi a Lagos na tambayeta ya haka tana kuka tacemin ko kuɗin motar dawowa arewa bai bar mata ba ita yanzu Damagaran takeson komawa cikin danginta haka na ɗauketa na kaita tasha na biya mata kuɗin mota tare da guziri ta tafi Damagaran yanzu haka dai tana Damagaran" cikin tashin hankali tace.

“Amma ciki fah kikace Janah?" Murmushi tayi tace “kuma ƙarin baƙin cikin ma tace bana Idi dillalin bane wai Wasu ne suka ganta a wahale shine sukace tazo gidansu ta rinƙa karɓar abinci kullum suna bata abinci harda ruwan wanka tayi wanka kinsan Inna idan taji gyara kyakkyawar mace ce gata jajir iya wuya bantaɓa ganinta tayi baƙi ba, a hakan ne ɗaya cikin mazaunan gidan ya ritsata wata rana yayi mata fyaɗe shine ta samu cikin kuma yace idan ta danganta shi da cikin sai ya kasheta ita kuma gudun kar su nemi rabata da rayuwarta kawai ta yanke

shawarar barin gidan shine ta fito tana bara tana kwana a ƙasan gada har Allah ya haɗata Dani watarana a kasuwa" Tashin hankalin da Batul ta shiga fasalta yawansa ma ɓata baki ne haka ta aje wayar Zuciyarta a jagule ta tashi tana zaga ɗakin, cikin shekara biyu abubuwa sun rikicewa rayuwarta tana ganin kamar ta samu sauƙi ashe akwai wata ƙurar a ƙasa, shigowar Samha ne ya sata tsayawa tare da zuba mata idanu, Samha ta tako gareta tace “Mene kuma yake faruwa?" Nufar wardrobe tayi ta buɗe tace “Dole ya zamemin neman visa don komawa Afrika cikin satin nan Samha idan kin shirya mu tafi tare in kina da abinda zaki ƙarasa na tafi Ni kaɗai" fahimtar yanda take a dame ne yasa batayi mata mgnr abinda ya kawota ba itama ta fara taya ta shirya kayan tace “Amma bamu sanar da gurin aiki zamuyi tafiya ba gashi kinsa mana tafiyar a ƙurarren lokaci" bata iya bata amsa ba haka suka gama suma kwanta washegari suka fita aiki kamar yanda ake ta shirye shiryen zuwan mamallakin rukunin gidajen abincin Na MB Kitchen's haka akaci gaba da gabatarwa cike da annashuwa ita kam batada walwala haka suka tashin washegari juma'a ta kama ranar da shugaban nasu zai shigo bata wani bawa zuwan nasa muhimmanci ba duk da cewa an sanar da ita idan ya shigo taron ma'aikatansa gabaɗaya yake haɗawa haka idan zai tafi.

Taje wajen aiki tayi abinda zata yi gaf da fara taron ta tafi ambassy domin gama shirye shiryen tafiyara Afrika daya rage saura kwanaki biyu ta tashi daga ambassy gida ta wucce saboda ciwon kai da faɗuwar gaban daga sarƙeta washegari asabar ce bata da aiki Samha ce ta fita ita kam a gida ta yini sai yamma ne wayarta ta fara rurin neman agaji tayi tsaki tare da danna gefenta cikin kwanakin nan kaɗaici yafi mata komai daɗi da wannan ko wayarta batason taji tayi rurin neman agajinta.
Bata dawo daga duniyar tunanin datayi nisa a ciki ba wayar ta ƙara ɗaukan ruri ta ɗauka a fusace ganin number ƙasar ce ya sanyata karawa a kunneta, sallama aka fara mata da ita ta amsa tare da Nutsuwa don tuna inda tasan Muryar, maimakon haka sai taji an sauke numfashi anci gaba da cewa “Ranki ya daɗe gani a harabar gidanku a taimakeni a zo a ji da menazo" sosai mamaki ya cika ta tasan wannan dukka sharrin Samha ne haka dai ta daure ta gyarawa Jany dake bacci kwanciya ta ɗauki ɗan ƙaramin hijjab ɗinta ta sanya ta nufi inda ake neman nata.
Tunda ta fito idanun Deen ke  kanta har ta ƙaraso inda yake tsaye fuskarta a ɗaure tayi masa sallama ya amsa tare da zubanta idanu tana ci gaba da latsa wayarta, dama baiyi tsammanin wata tarɓa me kyau a gare ta ba domin tunani yakan fidda kamanni bisa dukkan alamu yarinyar tsoron maza takeyi koda yake ga yanda Samha ta basa labarinta ya halatta na tayi tantamar sake yarda da wani namiji a duniya to amma ai ba'a cire tsammani kuma banda abinda shi dama farin banza ai a farau faraun banza yake ƙarewa, ita me take tsammani da mutumin da sukayi wannan rayuwar dashi, yafi mata sha'awar taimakon kanta ta gyara gobenta saidai ya fahimci kamar hankalinta baya zuwar mata da haka, but me nema baya ƙasa a gwiwa zai dage bakin rai bakin fama don ganin ya mallaketa halalinsa.

Ajiyar zuciya suka sauke a tare ta juya da nufin bar masa wajen domin ta tsargu sosai da kallon da yake yi mata, da sauri ya riƙo hannunta tare da janyota jikinsa ta faɗa ƙirjinsa yayi saurin riƙe ƙugunta yaja ajiyar zuciya me ƙarfi tare da ɗora bakinsa daidai kunnenta yace “Kyakkyawar fuska tana ƙara Armashi tare da murmushi gimbiyata don Allah ki daina hukuntani da laifin ƙaddarar da Allah ya jefoni cikinta a ƙarshe Fateemah koma mene Ni a haka nakeson ki zama sirrina kuma uwar ƴaƴana ki yarda ki bawa wannan ƙasƙantaccen bawan dama yaje dake ga iyayensa matsayin Sarauniyar data yarda ta rayu ƙarƙashin mulkinsa Fateemah nayi alƙawarin kare miki mutumcinki da ƙimarki har fitar numfashina na ƙarshe"
Zamewa yayi ƙasa ya riƙe Ƙafarta yace “Don Allah Mom Jany ki taimaki Deen ki damƙar rayuwarki data Jany amana a wajensa wlh bazanci amanarki ba, zan rayu ne yanda kikeso"
Tunda ya fara maganar ta zubansa idanu kyakkyawan saurayi Masha Allah son kowa yanayinsa yana fidda wata kala da akafi samunta a halpcase wato ruwa biyu yanada ƙirar ƙarfafa yanada suma kwantacciya wadda alama ta nuna rashin barinta ta taru sosai shine ya hanata zama irin ta larabawa, da gaske Deen ya haɗu.
Cikin kwanakin daya shigo rayuwarta babu abinda yake bata mamaki irin sanyin halinsa, duk wulaƙancin da take yi masa bai taɓa nuna ya damu ba abu ɗaya yake faɗa mata kullum Mom Jany (Walaƙad karramana bani adam) wannan cewar Allah S.W.T ce don Allah ki bani dama nasan bazan taɓa samun matsala da ke ba kiyimin alfarmar so Fateemah"

Rikita mata lissafi yake yi da kalamansa sannu a hankali ya fara cusawa Zuciyarta tausan sa wasu ɓangarori na ranta yana bata shawarar to ita me take jira da rayuwa ne? Da bazata nemawa kanta makoma ba kafin ita duniyar da kanta ta nema mata, idan tace Ma'eesh take jira har sai yaushe ne zai waiwayesu meye ya hanashi nemansu tabbas bata taɓajin a ranta Ma'eesh baya duniya ba ita dai tafi zargin duk abinda yake buƙata a gurinta ya gama samu ne shiyasa ya wofintar da rayuwarsu" da wannan tunanin taji ya sake riƙe hannunta yace “Damar farko kuma ta ƙarshe Fateemah don Allah...." Wani kuka ne me ƙarfi ya ƙwace mata da ya sanyata ture hannunsa ta nufi cikin gidan da gudu ta faɗa gado ta rushe da kuka me sauti tana yage hularta da Hijjab ɗinta, daidai lokacin da Samha ta shigo da uwar leda a hannunta ta aje tana cewa “Ananan ana sana'ar kenan? To Allah yabada Sa'a yayi miki tsari da makantar ƙuruciya domin tabbas baki daina kuka akan wannan Guy ɗin da alama ta nuna babu shi a wannan duniyar ba"

Sake fashewa tayi da kuka tace “Ya zanyi ne Samha so nake na saba da rashinsa so nake na cire shi a raina saidai na kasa ta ina zan fara ne?" Murmushi Samha tayi ta zauna a kusa da ita tace “Abinda nakeso ki tambaya kenan kika kasa Teemah matakin cire matacciyar soyayya a rai shine ɗaukan me rai kisa a samanta kiyi ƙoƙarin barin matacciya matsayinta Na mara amfani ki bawa rayayyiya power ta hanyar kallon masoyin gsky da idanun rahama Teemah tunda nake dake Deen shine mutum na biyu da ya nuna yana miki so irin na aure dama Hameed bai kai ba domin bashida nagartar zama abokin rayuwa but meye matsalar Deen ne idan kyau kike nema shima ya samu rabonsa Asalin ta inda kyau yake ya ɓullo mahaifinsa Balaraben Sudan ne Kano ne amma mahaifiyarsa Balarabiyar Labanon ce ɗan babban gida ne gidan addini gidan dattako gidan kamala kuma gidan arziƙi sannan shima ya tara nasa, gashi da sanyin hali da ɗabi'a wlh ranar da na sanar dashi wacece ke banyi tunanin zai dawo gareki ba sai gashi washegari ya dawo kuma yake faɗamin ya shiryawa aurenki har ya sanar da Abbunsa ya samu matar aure Abbunsa yace ya nema koda kaifin takobi ne indai kin masa suma kin musu duk kuwa da ya sanar da Abbunsa ƙaddarar data faɗa Miki shin Fateemah zakiyi wasa da wannan damar ki saki reshe ki kama ganye, bayan kinsan cewa yanzu duniya ta daɗe da tashi daga bacci mata sun daina damuwa da soyayya mafitar rayuwarsu kawai suke dubawa a aure ba soyayyar banza ba da so tari tafi tafiya a dararen farko na cin amarci Teemah ba sonki Nuraddeen yakeyi ƙaunarki yakeyi wadda ƙauna ita ke ɗorar da haƙuri da juriya a zamantakewar aure ba soyayya ba"

Sosai yau take fahimtar Samha hakanne ya sata ɗagowa tace “Ni kaina zuwa yanzu juriya ta ta fara gazawa Samha idan naƙi bawa Deen dama a kaina banyiwa kaina adalci ba domin dama bata cika maimaituwa ba saidai ina jin kamar naci amanar kaina da Zuciyata Samha har gobe Daddyn Jany shine kaɗai nakewa kallon namiji" share mata hawayen Samha tayi tace “Shi kika sani ne Teemah but shima akwai maza a gabansa fah wannan Guy ɗin daga yanayinsa in samu dama zai iya bai dake pri nursery a karatun namiji Yanada manyan halittu ga ƙirar ƙarfi ga kyau ga hatimin nasara"
Kasa sake cewa komai tayi ta koma ta kwanta Jany da Jalal da Samha keta buɗa kayan da Deen ya kawowa yaran itadai tayi nisa a duniyar tunani Saida Jany ta haura samanta tana cewa “Mom, Dad she's call you"
Numfashi ta sauke me tsayi kafin takai dubanta ga wayar still dai shine batason ɗagawa amma kafin ta gama yanke hukunci Jany ta kara mata a kunne suka sauke numfashi tare shiru ya ratsa tsakani kafin yayi ƙarfin halin cewa “Yaushe ne tafiyar taku?" A gajarce yace “Jibi" shiru yayi sannan yace “Naso tafiyar yazo ɗaya da tawa amma babu komai Nima cikin satin nan zan taho in yaso sai ayi komai a gama idan kika bani dama ma har bikin sai ayi mu dawo matsayin ma'aurata mu buɗewa rayuwarmu sabon babi ko?" Murmushi tayi ta ƙuta tace “Wai kai baka zuciya ne?" Dariya tambayar ta bashi ko babu komai yau yanada Sa'a tunda har tayi masa

magana, yace.

“Bamani da ita akanki Fateemah na matsu naga na mallakeki kinsan me? Tunda na haɗu dake bantaɓa cewa Allah ya zaɓamin alkhairi tsakanina dake ba abu ɗaya da nake faɗa masa ya gajarce mana wannan zaman yasa da wuri ki zama matata na baki baby ki haifamin twins" Dariya sosai ya bata tace "Shikenan and Ni nace Allah ya tabbatar maka da alkhairin dake tare dani Deen komai na rayuwa alkhairansa yafi ai" narkewa yayi kamar yana gabanta yace “Amma dai kin daina wahalar Dani yanzu zaki aureni ko?" Murmushi tayi tace “Idan Allah ya aura makani ya zanyi, Ni zaɓinsa nake nema" sunyi hira sosai shi kansa mamaki yakeyi tare da jin daɗin yanda masoyiyar tasa ta saki jiki dashi aje wayar sukayi tare da yi mata alƙawarin gobe zai zo yanason ya ganta matsayin wadda ta bashi damar ya zama jagoran rayuwarta.
Alwala tayi tasa kayan bacci ta kwanta Zuciyarta cike da tunani barkatai so take ta kawar da tunanin Ma'eesh kamar yanda kowa ke bata shawara saidai ta kasa duk kuwa da cewa itama batajin zata iya yafe masa wofintar dasu da yayi indai yana raye kuma lafiyarsa ƙalau cikin duniya, ta haƙura koda son sa zai zama ajalinta ta amince saboda abinda ta fahimta da rayuwa kawai ka rayu inda ake buƙatar rayuwarka" Washegari kuma da wuri yazo ya kawo mata uwar siyayyar da yayo musu ita da  Jany da Jalal idan yayi wani abin har tausayi yake bata gashi da kara bai taɓa siyawa Jany abu bai haɗa da Jalal ba wannan ya ƙara masa ƙima a idanun Samha taketa kafa masa gwamnatinsa, ranar Litinin kuwa zakara ya basu Sa'a a Nigeria suka sauka garin Kano suka kwana biyu tare da bawa Janah  manya kyautuka da kaita asibiti aka ɗorata akan magani ashe ma ba HIV ɗin bace sanyi ne yaci jikinta fiye da tunani, washegari sannan suka ɗauki hanyar Niger cike da zullumin abinda zasu tarar.........

_Am so sorry yau naje asibiti na gaji kuyimin haƙurin gobe_

*Paid book 500 VIP 1k via 9031307566 Fauziyya Tasiu Umar Opay Evidence of payment 09031307566.*

*Oum Hairan*
[7/8, 7:43 AM] Oum Hairan: SIGNED MARRIAGE
*_(Kalma ɗaya)_*

*Oum Hairan*

*___________________________________*
*Book 2 page 11-12*
*___________________________________*

Sun isa Niger da dare a babban birnin ƙasar suka sauka suka kwana wani katafaren hotel da safe suka shirya suka fito domin nufar Damagaran tun fitowarsu wata hamshaƙiyar mota take musu horn basu kula ba domin basu ma kawo dasu ɗin ake ba har Saida matashin buzun ya fito a motar cikin shigarsa ta buzaye ya iso garesu yayi musu sallama Samha ce ta amsa tare da kallonsa ya zame ƙallen daya rufe fuskarsa dashi saboda yanayin hunturun da akeyi ya kama hannun Jany yana mata wasa yace “Da alama ku ɗin baƙine ko zan iya sanin masaukinku?" Da farasanci yayi maganar Samha tace.
“Eh zamu karasa Damagaran ne can ammasaukin mu" ba tare da tunanin komi ba yace “Sara kan gaɓa Nima can nayi muna iya tafiya tare?" Da sauri Samha tace “Ah haba ai Bama ɗora maka nauyi ba kaje kawai muma muna tahowa" waya ya zaro yace da drivensa yaja motar ya tafi zai taho da baƙinsa" da sauri Samha tace “Aa kar ayi haka muje" Batul da batasan me suke tattaunawa ba Samha ta kalla tace “Muje Hajiya mun samu lipt zuwa Damagaran ɗin" bata ja ba duk da bata bada fuska ba saboda ta lura hankalinsa a kanta yake.

Address ɗin gidan ta rinƙa basu suna bi cike da mamaki Ansar zai yi magana Anwarr ya hanashi sunyi tafiya me ɗan tsayi sannan suka isa ƙauyen Yar kuka inda sukayi parking gaban gidan me unguwa suka fiffito suna kallon garin cikin shekara bakwai da tayi batazo garin ba matuƙa ƙauyen ya canza ga raƙumansu nan turke gaban gidajensu.
Wasu matasan buzaye sukaga sun nufosu ita dai bata iya gane wani cikinsu ba suna ƙarasowa suka fara gaisawa dasu Anwar ya tambaye su me garin yananan, nan suka sanar dasu yaje gona amma bashi jimawa yaka zakkuwa itadai Batul kallonsu tayi tayi musu Godiya ta nufi cikin gidan gabanta na faɗuwa Zuciyarta fal da tunanin irin kallon da zasuyiwa juna ita da Inna Laure, sallama tayi daidai lokacin da Inna ta fito daga makewayi, tana ganin tilon ɗiyar Tata ta saki butar ta nufi Batul da gudu tana cewa "ga Batula ga Batula" nandanan dukkan matan dake ɗakunansu suka firfito domin ganin ɗiyar data sallamu duniya yau a gidansu kowa kallonta yakeyi da mamaki suna kallon Jany da tsoron mutane yasata kanƙame mamanta tana kuka tana cewa a ɗauketa, Samha dake shigowa itane ta ɗauki Jany tana cewa da ita “Ke kin cika rigima Jany meye kuma na kukan?" Jansu Inna Laure tayi har ɗakinta itadai Batul kallonta takeyi cike da tsoro badan Inna haihuwarta tayi ba da bazata gane ta ba saboda muguwar ramar da tayi tunda take bata taɓa ganin Inna tayi baƙi ba sai wannan karon, haka suka shiga dakin da aka shimfiɗawa ledar buhu a ƙasansa da ɗan karamin gadon ƙarfe Inna ta kuma shimfiɗa musu darduma sunata kallon kallo da Batul bayan dukkan matan gidan sunzo sun

gaggaisa yaran ma sunata zuwa ganinsu suna cewa wai baƙin Turawa ne sukazo, to jiki yaci kuɗi sun saje da masu jajayen kunnen.

Kallon Nutsuwa Inna tayiwa Batul tace “Yanzu Batul akwai daɗin da zaisa ki manta Dani a duniya inanan abin duniya yayimin zafi nadama ta baibayeni inata tunanin ta inda zanjiki ko na ganki ke kuwa kina can kin samu guri kin manta dani" girgiza kai tayi wato har yanzu Inna tananan da ɓirɓushin halinta wai ta samu duniya ma take cewa ba tambayarta zatayi halin da rayuwarta ta shiga ba, murmushi kawai tayi ta share hawaye tace “Inna wannan ƙawata ce Kuma uwar ɗakina Samha a lokacin da aka saceni daga Nigeria aka kaini Austaralia bayan kin siyar dani a hannun matsafa sun ɗaukeni sun kaini can da zummar idan na haifi wannan yarinyar dake jikinki wadda kuka siyarwa da ubanta Ni na shekara biyu, su kasheni su kashe yaron da na haifa don cika burinsu na tsafi.

Nan ta kwashe labarin komai ta labartawa Inna Laure Aikuwa ta shiga tashin hankali da ɗimuwa tayi kuka kamar ranta zai fita ta rinƙa yiwa Samha godiya data gatanta mata ɗiyar tana.

Suna tsaka da wannan tattaunawa ne Mal Garbu da yake matsayin uba a gurin Inna Laure ya shigo, kasancewar shi ƙanine ga baban Inna Laure ya kalli Batul yace “Ke ar baƙauyiyar kawai kizo da baƙi ki barsu a waje badan ƴan gari bane Wagga ɗiya da tabawa mutane kunya Laure ɗiyan Alh Khamilu ƙanin me unguwa dake zaune a Niamey ne ya kawosu yaron nan mazaunin France Anwarr yake kamar ko?"

Dafe kai tayi tace “Kai tsohon nan har yanzu kananan da azarɓaɓinka to naga bani suka biyo ba wannan sarkin kwashe$^2$n ce ta ɗebosu" tashi yayi ya fita ya shigo dasu aka shimfiɗa musu wata dardumar suka gaisa da mutanen gidan har suna zolayar Anwarr yaushe zai yi aure ko sai ya gama cin bokon?" Murmushi yayi yana kallon Jumaire matar Mal Garbu yace.

“Inna Jumre Ni ai na samu mata a gidanki gani sai ki ƙwaɗani ki cinye dama rabonta ne ya hanani ganin kowa sai gashi yau nayi gamon Katar gashi cikin ikon Allah tuwonku manku ko ƙanwata?" Wata harara ta watsa mashi da ta sanya hantar cikinsa kaɗawa yayi ƙasa da kai Jumre tace “Kai kuwa Anwaru ina zaka kai Ta Manzo Wagga ɗiya da shaiɗan yayima fitsari a ƙafa ta zama karuwar ƙasa da ƙasa ita zakace zaka ɗiba to kuwa kasan kaima uwayenka basu barinka saboda haka ka ruha mamu asiri ka barmu mu ƙarasa da ƙwarinmu"

Koda bashi aka faɗawa maganar ba Saida ta girgiza shi kuma ta ɓata masa rai ya kuwa haɗe rai yayi shiru itama ganin kallon da Mal Garbu yake yi mata yasata lallaɓa tsufanta tayi gaba abinta.

Tashi Anwar da Ansar sukayi sukai masu sallama da cewar zasu dawo zuwa dare  dai lokacin ne suka samu hutawa sukayi wanka sukayi sallolinsu duk da cewa duk basu nutsu da gidan ba da alama Inna ba zaman lafiya sukeyi da mutanen gidan ba sai zubar musu da maganganu sukeyi suna yan waƙensu na mutanen ƙauye na habaici, itadai Inna tsumu a ɗaki bata cewa ƙala ganin abin nasu bana daraja bane ya sanya Samha samun Batul tace mata "Nifa ba komi raina yake ɗauka ba Teemah duk da cewa Innanki tayi kuskure amma bai kamata zuwanki yasa waɗannan ƙauyawan matan suyita yi mata ɗan bikin nan ba magana ta Allah zan kira Anwar yazo su nema mana hotel mu kama idan kuma da wani abu da za'ayi to ayi amma idan naci gaba da zama a wannan gidan tsaf zanmusu duka" share hawayen daya zubo mata tayi tace "Nima bazan iya zama a nan ba kinji fah yanda suketa ƙyararmin Jany duk taƙi sakewa sai kuka take yi" kiran Inna sukayi Samha ta sanar da ita sufa zasu shiga gari su nemi masauki "Nan Inna take faɗa masu suyi haƙuri Haladu ƙaninta yazo ta karɓi mukullin gidan Mahaifin Batul ɗin da tasa aka kwaskware zata koma ciki da zama itama zaman gidan ya isheta kullum sai sun sata kuka akan rashin Batul ɗin yanzu kuma ta dawo da yarinya tasan abin ƙaruwa zai yi" haka akayi Halliru yana zuwa ya rakasu ba laifi gidan yafi wanda suka baro kyau domin ginin zamani ne ya gama ginawa kenan zasu dawo Yar kuka da zama Allah yayi masa rasuwa dake sunyi canjin kuɗi sosai a Kano haka suka cire kuɗi aka siyo musu katifu guda biyu manya six by six sai ƙarama guda ɗaya ta yara suka sanya ɗaya a ɗakinsu ɗaya a ɗakin Inna gefe suka saka ƙarama ta yara suka saka glub aka simunte bayin cikin kwana ɗaya suka mai da gidan yanda sukeson ya kasance kafin su tafi domin kuwa tuni Batul tasa a nema mata gida a Kano kuɗaɗen da suke account ɗinta da Ma'eesh ya zuba mata sunada nauyi sosai sannan ga na wajen Lateef suma batayi komai dasu ba Gara ta nema musu gida inda babu wanda ya sansu su zauna su nutsu su nemi mafitar rayuwarsu.

Da safe sukaje gidan me unguwa inda nan ne aka haifi Mal Daheer mahaifin Batul sosai sukayi murnar ganinta Musamman kakarta mahaifiyar babanta da mugun halin Inna Laure yasa basa ga maciji dake tun jiya sun san da zuwanta gurin Anwar da yake matsayin abokin wasa gareta domin da Mal Ɗaheer  da Alh Halliru yan turaka suke ma'ana ubansu ɗaya zumunci ne dake bayinsa sukeyi ba domin shi Mal Ɗaheer da baƙin halin Inna Laure ya ishi danginsa sukace sai ya sake ta ne shi kuma yace yanason matarsa bazai rabu da ita ba ta wannan sukaji haushi suka sallamawa Inna shi shine dalilin da yasa ko sun shigo ƙauyen Ƴar kuka Inna bata bari Batul taje ta gaida dangin mahaifinta kwatsam kuma sai gashi lokaci guda Inna ta sauko. Tunda sukazo kullum suna maƙale da Deen a waya nan yake gaya mata shima nan da kwana huɗu zai taho, a ɓangare ɗaya kuwa Anwarr daya taho Damagaran da niyyar kwana ɗaya sai

gashi ya nemi gurin zama duk da cewa Batul taƙi bashi fuskar yace mata komai amma matsayinsa na ɗan uwanta yasa bata wulaƙantashi.
Kwanansu biyar da zuwa Deen ya kiratd yake cewa da ita yana Damagaran ta bashi address, sosai suka cika da mamaki matuƙa nan take bashi kwantancen inda za'a kawo shi ta tashi ya shiga wanka ta fito ta sheƙa kwalliyarta cikin shigarsu ta buzaye.
Tana tsaka da shiryawa Anwar ya shigo ya tsaya yana kallonta ta ɗago tayi masa murmushi tace “Yada kallo haka Yaya Anwar?" Ajiyar zuciya yayi yace “Aa babu komai wankan ne ga kin karɓeshi Masha Allah"

*Contact me*
*09013718241*

*OUM HAIRAN*
[7/8, 10:29 AM] Oum Hairan: *SIGNED MARRIAGE*
*_(Kalma ɗaya)_*

*Oum Hairan*

*___________________________________*
*Book 2 page 13-14*
*___________________________________*

Ajiyar zuciya tayi tace “Allah da gaske nayi kyau da shigar gado na, wow! Hammah Anwarr kace zanja magana...." Numfashinta taji yana barazanar ɗaukewa tayi maza ta dawo hayyacinta ta sauke idanunta kan Anwar daya ƙure mata guri numfashinsu na dukan juna ya sanya hannu yana zagaye lips ɗinta tare da janyota ya shigar da ita jikinsa ya ɗaga kanta sama yace “Kalli waɗancan tsuntsayen Batul basu burgeki gani ba?" Ɗaga kanta tayi ta zubasu kan wasu kyawawan tsuntsaye da ko a Turai bata taɓa katarin ganin ƙananun tsuntsaye masu kyawunsu ba bakinsu yana cikin na juna ɗayan yana rerawa ɗaya kukansa me jan hankali, sosai tsuntsayen suka sanyata a shauƙi sosai ta kamu da sha'awarsu da kewar abinda sukeyiwa juna, ta kuwa lafe a jikin Anwar me fitar da wani sihirtaccen ƙamshi me kashe jiki.
Bata fahimci abinda take aikatawa ba Saida taji saukar Muryarsa a dodon kunnenta yace “Kamar haka ya kasance Ni dake ne ƙanwata cikin wannan shauƙin da begen rayuwar da zanji daɗi zanji kamar nafi kowa Sa'a, saidai baƙin cikina nasan kin fahimci me nake nufi amma kinƙi

nunamin ganewarki bari nasa ran zaki juyo ki dubeni, Batul Ni ba yaro bane shekaru na sun fara nauyi fah inada shekaru talatin da biyar na kusa alba'in kinga dole ina buƙatar abokiyar rayuwa, wlh ban fahimci haka ba Saida idanuna ya sauka a kanki, dama zaki bani dama tabbas da na nunawa duniya irin saarki da kika sameni matsayin abokin rayuwa"......

Tureshi tayi ta nufi ƙofa zata fice ya sake cafkar hannunta yace “Laifi ne don na buɗe maki Zuciyata Batul meye ne kikeso na baki shi wlh Ni ke kaɗai nakeso ki bani dama kinsani komai son da wani zai nuna Miki bayakai yani da jininmu yake gudana iri ɗaya don Allah ki bani dama Batul"...... Ficewa tayi daga ɗakin ta nufi ɗakin Inna inda suke hirarsu ita da Samha tanawa Jany kitso tana cewa “Yo ace a barwa yarinya kai ba'a kumbushe matashi Wagga wannan suma mu a nan ai baki lalata zaiyi"....... Faɗowarta cikin ɗakin ne yasa Su Inna miƙewa suna tambayarta “menene?" Tsayawa yayi jikin ƙofar “Bafa wani abu bane Inna kawai don na roƙeta alfarma ne shine take wannan abin Wlh Inna Inason Batul kuma ina raye bazata tafi dangin wasu ba"
Murmushi Inna tayi tace “Anwaru kenan ba laifi bane don kaso ƴar uwarka amma kasan ƙura zaka tayar idan maganar nan ta fita sanin kankane uwayenku basasona bare su so halwata, ta yaya kake tunanin zasu yarje maka auren ta Manzo?" Sosai zuffa take keto masa amma dake Buzun gaske ne sau cewa yayi “Nifa Inna zata soni to kowama ya barni bana neman tallafin kowa wajen kula da iyali na" daƙyar Inna ta lallaɓashi ya tafi sannan itama ta fito suka dubi juna da Samha, Samha tace “Ke kiji wata lukutar masifa Teemah wannan Anwar ɗin da gaske gaɓo ne daga ganin Sarkin fawa sai miya tayi zaƙi kuma fah akwai ƙura wlh don jiya da mukaje gaida Inna Yaure Tayi wata magana dana kasa gane  me take nufi lokacin da take cewa “Tunda Allah yasa kin dawo cikinsu basu kuma bari kiyi nisa dasu zasu sama Miki Samrayi cikin Samarinsu buzaye su amra miki kin tuna lokacin kuma kinsan lokacin Anwar da Mustapha suna wajen suma har sun kalli juna kallon dana kasa gane wanne iri ne inda Mustapha yayi saurin cewa “Inna Inaso nikam in za'a bani shi kuma Anwar yayi ƙwafa ya fice kin tuna?"

Numfashi ta sauke tace “Ina sane Samha duk wannan abinda sukeyi ai babu wanda ya Isa goge zanen ƙaddara Ni har yanzu fa banjin akwai mijina a cikinsu kawai dai suna abinsu ne in banda haka Ni yanzu yama za'ayi ace za'a min aure a zaunar dani a ƴar kuka suma sun san bazai yiwu ba, ke nifa gabaɗaya Niger ma ba taƙamarsu Niamey ba to Ni batamun a zama ba"
Wayarta ne ya shiga ruri tana dubawa taga number Deen ta kalli Samha tace “Deen ne kije gareshi ki shigo dashi" fita tayi iya kuma ta koma ɗakin Inna ta ɗauki awarwaronta ta saka tana

fitowa suna shigowa idanunsa a kanta tayi saurin janye nata tana murmushi, ya sauke ajiyar zuciya ya shiga inda aka saukeshi bayan sun gaisa da Inna ya zauna itama ta shigo da sallamarta ya amsa idanunsa na kanta tana shirin zama ya riƙo hannunta tare da zaunar da ita a gabansa ya saki wata ajiyar zuciya me ƙarfi yace “Alhmdllh Fateemah ranar da za'a kaiki gidana irin wannan dressing ɗin zakiyimin wlh kin tashi kaina kin jiƙamin aiki ji nake dama abani dama yau ɗin nan!"

Cike da kunya ta zame hannunta ta zauna tana sunne kai kamar wata muminar gaske tace “Noor kasha hanya, ya gajiya" lumshe idanunsa yayi yace “Bangaji ba sai yanzu dai kike gajiyar Dani" Sosai sukayi masa sauka me kyau shayinsu na buzaye shine yafi komai burgeshi yasha shayi babu ƙarya a ƙarshe yake faɗa mata Sudan zai wucce ya dawo ya tarar Mom da Dad duka suna can daga can kuma zasuyi waya da ita a basu lokacin da zasuzo ayi komai a gama a tsayar musu da lokacin bikin.
Itadai batace masa komai ba haka Inna tace ta rakashi ya gaisa da uwayenta suna tafe cikin garin cike da shauƙin juna zuwa yanzu da gaske zuciyar Batul ta fara buɗewa a hankali ta fara koyawa kanta soyayyar Deen, yanda hadari ya lulluɓe sararin samaniya ya ƙarawa yinin masoyan armashi suna tafe suna hirarsu ta ƙauna har suka isa gidan me gari sukayi Sa'a yana zaune a faɗa shida yan uwansa suna ganinta suka washe baki Baffa Lame yace “Aa ta Manzo yanzu muke tamtamnawa akanki sai gaki dama ɗiyan halak yaƙi ambato kice baƙo kikayi daga birni" zama tayi cike da kunyar iyayen nata suka gaisa da Deen tayi ƙasa da kai sunason tayi masu bayani ita kuma kunya ta hanata.
Sai shine yayi ƙarfin halin gabatar da kansa sukayi shiru na lokaci kafin daga bisani Mal me gari yace “Ta Manzo bamu guri ko?" Cike da girmamawa da kunya ta tashi ta fice tana fita Suka haɗu da Almustapha a ƙofar fada yace “Yawwa amaryata dama yanzu nake shirin zakkuwa gareki ance kinyi baƙo daga Nigeria cikin ɗiyan iskan da sunka ɓata mani rayuwarki ko? To maza ki dakatar dashi zowa gareki ki hwaɗi masa niya ammijinki yanzu haka taɗi yaje gaba ga manya kinjiya"

Wani mugun kallo ta watsa masa tayi gaba abinta Zuciyarta na rawa ita kam bata yarda da wannan zama da akace Deen yayi ba to me zasu hwaɗi mashi da sai batta gurin?" Ji tayi an damƙi hannunta ta juya taga Mustapha ne yake mata wani kallo yana washe mata baki takaicin yanda yake mata kallon ne yasa batasan sanda da zuba masa wani mari ba, ta ja da baya da sauri tana huci idanunta ya kawo ruwa tace “Mustapha tun ranar da na shigo garin nan nasan akwai irinku da yawa marasa tarbiyya marasa ɗa'a kuma marasa manner ta furuci, don Allah kar mu ƙara gauraya dakai a gonata zan keta alfarmarka....."
Cikin bala'i yayo kanta Anwar dake tsaye nesa dasu yayi saurin janyeta hakan ya kara fusata

Mustapha yace “Har kece zaki cewa wani bashida tarbiyya shin ke waye ya baki tarbiyyar Sallamamen Uban naki da shima bai isa ba gurin gyatumarki ko kuwa ita Laure idon Naira ɗin ce ta baki tarbiyyar da saboda kin kwankwaɗi ta har kikayo ɗiyan dakan kuka a gantalin barikin naki yo bandama anason taimakonki mi zaayi dake Ni aggareki balle ki bani guri duk an rarakeshi......"
Wani marin Anwarr ya zabga masa daya sanyashi zubewa a ƙasa yana tashi kuwa ya zare takobin dake rataye a jikinsa yayi kan Anwar ya ɗaga zai buga masa tayi kukan kura ta shiga gabansa Aikuwa Allah ne ya kiyaye ya sauke mata ita a allon kafada a Anwar ɗin yayi mata daukar jaririya ya kauce da ita daga gurin shima ya zare tashi takobin yayi kan Mustapha yana huci abinda ya sanyata fasa ƙarar data sanya uwayen nasu fitowa daga zauren Mal me gari daƙyar suka raba rigimar suna muzurai suna cin ƙwafa kowa aka janye shi inda ita kuma Deen yazo ya kama hannunta suka bar gurin duk jikinta yana rawa.

Inda motar data kawo shi take nan suka nufa har yanzu kuka takeyi wannan shine karo na uku a zamanta na sati ɗaya a garin nasu da akayi mata gori akan ƙaddarar da bata zaɓeta da kanta ba sosai ranta yayi kunci takejin bazata yafewa duk wanda yayi silar ɓata mata Future ta rayuwa ba, durƙushewa tayi ta saki wani marayan kuka daya ƙara tashin hankalin Deen daɗi da wanda yake ciki ya tsugunna gabanta yace “Sunce bazasu bani aure ba Ni bare ne, sunce sunada samari a wannan dangi da yawa marasa aure ciki ma akwai biyu da suka nuna suna son aurenki Fateemah na fito da wannan raɗaɗin tashin hankalin me maimakon ki kwantar min da hankali sai ki ƙara jefani a tashin hankali meye yasa zasu hanani ke bayan na riga na gama lissafa rayuwata dake Fateemah don Allah kar su rabani dake kome sukeso xanyi musu in sunaso na dawo rayuwa a cikinsu ne ma na yarda a nemamin fili xanyi gini zansai raƙuma zanyi naɗi Wlh Fateemah har yawon tallan kanwa in sunaso zanyi inda akanki ne"
Sake rushewa tayi da kuka tace “Meyesa ƙaddarata ta zama mummuna Deen ban zaɓi rayuwata ta zama a haka ba, ban shiryawa ƙaddara me muni ba amma ya zanyi an gina rayuwata da tubalin toka yayi kyau amma daga ƙarshe bai ƙarko ba Nuraddeen bantaɓa riskar rayuwa me ƙunci irin rayuwar da nayi da Daddyn Jany ba duk kuwa da na soshi bantaɓa tunanin gujewa muradansa ba duk kuwa da nasan gaba zasu ƙalubalanceni, Nuraddeen Meyesa bazasu barni nayi nesa dasu ba zasuce a cikinsu zasuyimin aure bayan duniya bata taɓa yimin goron ƙaddarata ba Saida na dawo cikin dangina, ƙaryane Nuraddeen bazan iya aure a wannan ahlin ba ko kowa bazai fahimceni ba ni zan fahimci kaina so nake Jany ta rayu kamar kowa taya zan yarda da rayuwa cikin mutane masu ƙabilanci irin DANGINA"........

Idanunsa da suka kaɗa sukayi jawur ya ɗago yace “Yaushe zaki koma Austaralia?" Girgiza masa kai tayi tace “Bana burin sake barin ƙasata batare da aure ba ina gudun ƙaddarar da tafi wacce ta gabata muni ta faɗo rayuwata don Allah Nuraddeen don Allah ka yarda duk wuya kace saini nima zance sai kai bayan iya karɓar ɗayan waɗanda suke shirin zaɓamin ba"

Share mata hawaye yayi yace “Ba gudu ba ja da baya sai sun bani rabona da ya ratso ta hannunsu ko suna so ko sunaƙi Fateemah ke ɗin tawa ce" haɗe bakinsu yayi guri ɗaya Saida numfashinta ya ɗauke saboda wani sinadari da ɗanɗano da bazai taɓa gushewa a ƙwaƙwalwarta ba ta janye da sauri tana gwama numfashi yayi mata murmushi yace “Special gift ne My Zumata yau sai nayi wanka idan naje masauki na ko zaki rakani ki ƙarasa ladanki!?" Ya ƙarashe maganar yana narkar da murya ta rufe idonta da hannunta tana masa dariya ya shammaceta ya ɗagata cak ya azata saman motar ya sake ɗora bakinsa saman dokin wuyanta yasa harshensa yana lasar wuyanta yana sakin wani numfashi me tada mata hankali.
Wani irin rikicewar ƙwaƙwalwa take samu lokacin da yake mata komai sai takejin salon Ma'eesh hatta ɗumin harshensa bai saɓa dana Ma'eesh ba da sauri ta sake tureshi ta rintse idanunta tace “Wayyoh ka bari don Allah Noor!" Cikin sarƙewar murya yace “Sai yaushe?" Da sauri ta buɗe idanun ta tar a kansa tana masa kallon tsaf brand ɗinta na yamutsawa tana ƙara shiga bala'i hatta sautin nasa na yanzu sautin Ma'eesh ne, hannun da yasa yana zagaya idanunta shine ya dawo da ita hayyaci yi firgigit tace “Kaine Noor?" Da rashin fahimta yake kallonta yace “Nine mana Fateemah na canza ne?" Dirowa tayi daga saman motar tace “Zamuyi waya Noor"

Tana faɗin haka ta shige gida ya bita da kallo yana murmushi tare da addu'ar Allah ya nuna masa ranar da zata tabbata tashi forever, tana shiga gida ta fara watsi da kayanta tun daga kan mayafi har zuwa dankwali zuwa awarwaro da komai ta zube a saman simintin ta fasa ƙarar data fito da Samha da Inna da yaran daga ɗaki da gudu suka nufota ta faɗa jikin Samha tace “Waini Samha anya Ma'eesh ba aljani bane Meyesa duk sanda nake tare da Deen yakemin gizo"
Sake rushewa tayi da kuka tace “Wlh har ɗanɗanon yawun bakinsu iri ɗaya ne hatta ɗumin jikinsu Samha kodai bazai bayyana kansa bane yake zuwar min a siffar Noor?" Dariya sosai abin ya bawa Samha Inna kam ficewa tayi domin maganar ba Tata nace, Samha tace “Mutum ne kamar ke kawai kin ƙwallafashi a ranki ne shiyasa Deen yake Miki kama dashi a wannan fannin but ai har yanzu baku kai ƙarshen wasan ba da Deen sai anan ne zaki bambance" wani kallo takewa Samha tace “Kina ɗaukar kamar wasa ko wlh tallahi da gaske nakeyi Deen Komansa yanamin kamar na Ma'eesh ne" cikin fusata tace “to wai meye ne inma yayi Miki ɗin ai dama abinda kike nema kenan kuma kin samu kuma naga shima Ma'eesh ɗin kince mamansa Yar Sudan ce to kika sani ko sunada relation ta wani fannin ko kuma haɗin country yaja musu gamayyar Yanayin halitta"
Ganin Samha bata fahimceta ba yaɗata tashi ta nufi bayi tayi fitsari tayi alwala iya ɗan taɓatan da yayi har ta jiƙe itakam ta rasa irinta ko ya namiji ya raɓeta sai yaji shauƙin son kusanci ya kamata duk kuwa da kokarin dannewa da take yi da kuma hana abin tasirantuwa ga yanayinta, sallah tayi sannan ta kwanta yunwa yakeji amma ta kasa cin komai sai bayan komai ya lafa ne take bawa Samha labarin abinda ya faru tsakaninta da Mustapha da kuma hukuncin dasu baba me Gari suka yankewa Deen but yace babu gudu babu ja da baya zai Turo manyansa Azo ayi magana ɗaya ko su bayan ko kuma su faɗi me sukeso ayi musu ya amince zai yi".............

*Paid book 500 VIP 1k via 9031307566 Fauziyya Tasiu Umar Opay*

*Contact me*
*09013718241*

*OUM HAIRAN*
[7/8, 8:12 PM] Oum Hairan: *SIGNED MARRIAGE*
*_(Kalma ɗaya)_*

*Oum Hairan*

*______________________________________*
*Book 2 page 15-16*
*______________________________________*

Washegari da safe suna kwance a ɗaki Mal me gari yazo gidan da kansa yasa akayi masa iso Inna tace ya iso ciki haka ya iso Inna ta shimfiɗa masa taburma ya zauna suka gaisa yace “Ina ta Manzon ko basu tashi ba" fitowa Batul tayi tace “Gani Baffa na tashi tun subahi ban koma ba" amsawa yayi da cewa “To to ta Manzo hakan yana da kyau dama komawa baccin safe Na mara rabone ai" gaisawa sukayi ta nufi bakin mafitar ruwa ta tsugunna tana brush.
Mayar da hankalinsa ga Inna yace “Dama duba da cewa kinada haƙƙi akan ɗiyarki ta Manzo yasa nace zanzo da kaina na sanar dake hukuncin damu waliyyanta munka yanke game da amrenta Duba da abinda ya faru tsakaninta da yaron nan Mustapha ɗan wajen Lame yasa muka fahimci idan anka amra mata shi ma bassu zaman lafiya shiyasa mukaga tunda dama wannan yaron Anwarr ya nuna shima yana da soyuwa gareta a massashe da amren kansa, to Alhmdllh mun kira Alh Khamilun mun gumtsa masa kuma shima yayi fatan alkhairi yanzu dai an tsayar da lokaci ɗai da amren su Ladiyo da Jumme sai ki fara shiri kema"
Batul da tunda ya fara maganar tayi zaman dirshan a gurin ta ɗago da sauri tace “Amma Baffa saboda kar hakan ta faru nikkawo maku zaɓina jiya kuma yace zai turo uwayensa cikin satin nan...." Daƙuwa Inna tayi mata tace “Ungo nan ta Manzo ince dai Maigari shine madadin ubanki dukkuwa duniyar nan shine ya faɗa kike maida masa?"  Durƙushewa tayi gaban Inna tace “Wlh Inna bana fatan wannan dalilin yasa na ƙara maki nisa ban iya auren kowa a duniyarga inba Deen ba, Meyesa zaku yimin dole, bayan baku sabarmin da hakan ba ɗai wollah bani amren

Anwar saidai kowa ya haƙura wahala tau ce bata shuɗe ba"

Gwaɓe bakinta Inna tayi tace “Bakiyin shiru ke nan" cikin fusata Baffa Maigari yace “Yo in batayi haka ba ya za'ayi mu gane Ita wacece Laure ai hakan shine yake tabbatar mana da irin nonon da ta tsotsa da irin tarbiyyar da ta samu to dama barewa tayi gudu ɗiyanta yayi sassarhwa ai Idan batayimin haka ba bazan tabbatar da itan jinin Ɗahirun Inna Yaure da Lauren Buban Bugaje bace mutanen da suka zaɓi fita daga danginsu don su rayu babu me sanya musu idanun su tsula tsiyarsu son ransu, Laure sai Ta Manzo tayimin hakan zan tabbatar da ita ce yarinyar nan da aka cire mana Zakka a dangi ta shiga duniya har ta kawo mana ɗiyan shege cikin ahlinmu ba, banji haushi ba ko kaɗan Laure irin tarbiyyar data samu kenan saidai kuma ihun kurwa baya hana ruhi motsi tunda na riga na zartar sai an aiwatar in ba haka ba to saidai ta koma inda babu ƙwaɓar taci gaba da rayuwar da shi farkan nata data kawo mana wai har yana ce mana shi amrenta zaiyi yo wanne aure ne bayan gashi har ɗiya sun haifa dashi gashinan yarinyar haske ne kawai tayo na uwarta amma kama da komi daka ganshi kasan shine yayi cikinta da rana ma domin in dare ne da an samu cuɗin kamanni"

Kuka sosai Batul takeyi haka ya tsallaketa ya bar gidan yana jaddadawa Inna sati Uku saura bikin don haka su fara shiri Niamey za'a kai amarya Anwar ya riga ya gama gininsa daganan zasu wucce France tunda acan yake zaune" Samha ce ta kama hannunta suka koma ciki ta zube a katifar tana wani irin kuka me gunji tace “Anwar fah Samha wlh bazan aureshi ba saidai su kasheki"
Murmushi Samha tayi tace “Mukam zuwa cikin waɗannan bauɗaɗun mutane baiyi mana rana ba munyi gudun Gara mun haikewa zago wai dama duk dangin uba haka suke ne Teemah ko namu ne a haka? Shin ɗiyansu Ladiyo da Jumme suma amren dolen za'ayi musu ko kuwa sai ke da bakida gata?" Cikin kuka tace “Samha mubar garin nan" da sauri tace “ina zamu Batul da ranar auren wani a kanki?" Ta miƙe ta fara haɗa kayanta tace “Ban shirya zama ajalinsa ba ban kuma shirya ɗaura kambun mutuwa ba shiyasa nace Miki mu bar musu garinsu sai suyiwa wata amren dolin but wlh duk duniya namiji ɗaya ne zaɓina da ban sameshi ba na riga na haƙura a barni na rayu da wanda raita ta karɓa take fatan ya zama madadinsa"
Murmushi tayi tace “Kar muyi gaggawa Batul mu jira zuwan Uwayen Deen muga irin karɓar da zasuyi masu daganan kuma sai muyi abinda ya dace" bata kuma cewa komai ba ta zauna tana yamutsa sumarta tace “Oh God! Samha Meye laifin Deen ne da zasu ɗora masa abinda babu ruwansa Samha wlh shima ba sonsa nakeyi ba na zaɓeshi ne da fara koyawa Zuciyata sonsa don mafitar rayuwar Jany kamar yanda kika bani shawara, taya ma wai zan yarda nayi aure a wannan bauɗaɗen dangin? Waini ko bazanyi farin cikin bane na haƙura"

Cikinsu babu wanda ya kuma magana sun ɗauki lokaci a zaune ko break sun kasa daga ƙarshe suka shirya samun shiga gari suyi shopping suna fita suka haɗu da Anwar daga kallon da yaga Batul nayi masa yasashi sanin lallai saƙo ya isheta yayi murmushi yakai hannu zai ɗauki Jany ta janye ɗiyarta ta ɗagata tayi gaba sai Samha ce sukayi magana yace su jirashi yazo ya kaisu amma fir Batul taƙi haka dole ya ƙyalesu ransa babu daɗi shikam baisan meye yasa Batul taƙi karɓarsa ba, duk kyansa duk gatansa ace a cikin danginsa ne mace take nuna masa tsana bayan duk matan da ke bibiyarsa.
Komawa yayi gidansu ya shige ɗakinsa ya kwanta yini sur bai fito ba shirun Inna Hari taji tayi yawa ko abincin rana bai fito yaci ba, hakan ya sanyata shiga ɗakin ta iskeshi kwance a ƙasa ya zubawa selling idanunsa da suka kaɗa sukayi jawur ta zauna a gefensa yace “Anwar Kai baka iya sanya abu a ranka ba kaima irin ubanka ne Ni wlh banga abinda zaisa ka damu ba bayan dai gata nan ta kusa zama taka" zuba idanunsa yayi kan Inna Hari ya miƙe zaune yace “Da gaske takeson Guy ɗin tunda na fahimci ba don farin cikinta sukeson rabata da zaɓinta ba don wata manufa ne sai naji Gara na haƙura na barta ta zaɓeni da kanta nasan nafisa cancanta" Numfasawa yayi yaci gaba da cewa “saidai kuma bakin alƙalami ya bushe Mamee sun ƙara rura wutar ƙiyayyata a zuciyar Batul bantaɓa son abinda nakejin zan iya ɗaukar kowacce kasada akansa ba sai akan Batul amma Mamee hakan zai faru ne idan bata ɗaukeni a yanda ta ɗaukeni yanzu ba Inason na rayu da ita ne rayuwa me daɗi saidai ita tanamin kallon takobin dayake shirin sare farin cikinta garata Mamee inajin kamar na haƙura banson amsa sunan azzalumi tun a neman amre zataci gaba da kallo na a haka ne har cikin amren"

Shafa kwantacciyar sumarta tayi tace “Meye kuma Azzalumi Anwaru bakai ne azzalumi ba uwayenta ne kuma kasan Hwaɗuwar gaba asarar namiji ka dake idan ka ɗauka zata sauko itan ɗiya mace ce Anwaru (Hal jaza'ul ihsanu illal Ihsan) sakamakon me kyautatawa a kyautata masa inada tabbacin idan da irin mu'amalarka zaka mu'amalanci Ta Manzo wlh sai tasoka fiye da son da takewa wannan Sudanies ɗin kaidai ka wasa zuciyarka ka ƙarfafa ƙaddararka Ni wlh tamsayi kaka bani wannan bazaurar ɗiya duk ta susuta mana samarinmu Ni har yanzu banga irinta ba......"
A Hassale yace “Zaki fara ko Mamee bazan ɗauki taɓa martabar Batul ba, ko mece inasonta a haka haba don Allah Bama dole taƙini ba tunda tazo wannan garin kujera jifanta da munanan kalamai wai mutum yakan iya canza ƙaddara tai ne?" Murmushi tayi tace “Aa Anwaru ayi haƙuri Ni banƙin Ta Manzo kawai dai yanda ka susuce ne yake bani mamaki cikin kyawawan buzayen ɗiyoyin dake wannan gari an baka kaƙi yau kuma gaka kwance kakai kanka inda baka da gurbi" bathroom ya shige itama ta miƙe ta fice daga ɗakin ta kawo masa abinci bai ci na kirki ba yanayi yana duba agogo.
Sukuwa suna fita suka nemi abin hawa ya fitar dasu cikin garin Damagaran tare da kiran Deen sukaji inda yake suka karasa suka gaisa sun jima tare dashi sannan ya shirya suka fita kasuwar sukayi siyayyar Samha ce tayi musu siyayyar suko guri suka samu suka tsaya ya dubeta sosai yace “Wani abu ya kuma faruwa ne My Zumata?" Ajiyar zuciya ta sauke tace “Yaushe zaka tafi?" Murmushi yayi yace “Munyi magana da Dad yace na zauna gobe zai shigo Niger zasu

taho da yayansa sai suje garinku su nemamin aurenki" ajiyar zuciya ta sauke tace “Naji daɗin hakan saidai Allah yasa su amince" nan ta sanar dashi abinda suka yanke, yayi ajiyar zuciya yace “Basu canza hukuncin Ubangiji Fateemah mu barwa Allah shi yasan me yake rubuce a allon ƙudura" da wannan sukayi sallama suka nufi gida shi kuma ya koma masauki.

Tunda suka koma ko a ido taƙi yarda Anwar ya sanyata in ya kirayi wayarta ma bata ɗagawa haka suka cinye kwana biyun da rana kuwa Noor ya kirata yace ta faɗawa su Baffa Maigari ga baƙinsu nan, haka ta sanar da Bana Haladu shine ya sanar dasu zuwan baƙin suka shigo garin da jiniyarsu suka parker tarɓa sosai suka samu gurin su Baffa Maigari sannan suka zayyana musu abinda ke tafe dasu sukayi shiru na tsayin lokaci kafin daga bisani Baffa Maigari yace. Munyi tunanin zai sanar daku gskyr abinda muka sanar dashi da bai wahalar daku ba Alh wato wannan yarinyar mun riga munyi mata miji yanzu haka bikin ma saura sati biyu da yan ɗoriyar kwanaki kuma kunsani bisa ga al'ada in ba dole ba yarinya ta rasa masoyi cikin dangi mu Bama kai iri waje gonar gida bata shuku ba saboda haka muke baku haƙuri wahalar daku da wannan yaro yayi yarane na zamani kai haifesu baka haifi halinsu ba, itama haka muke fama da ita shiyasa ma mukaga Gara mu bada ita a gida a rinƙa kwaɓarta ana mata tsawa"

Duk yanda Abbuh da ɗan uwansa zasuyi sunyi abin yaci tura haka suka tashi jiki babu ƙwari sukayi musu sallama suka tafi basu sanar da Deen abinda ke faruwa ba Saida suka haɗu a Sudan suka zaunar dashi sukayi masa nasiha tare da nuna masa ya haƙura ya nemi wata tunda sunce bazasu bawa bare ba inda shi kuma yakejin duk kalmarsa ta ya haƙura kamar suna watsa masa dalma a zuciyarsa haka ya tashi jikinsa a mace ya shige ɗakinsa yaja bargo ya ƙudundune zazzaɓi ya sauko masa wannan lamari yayi kama da neman rayuwarsa waɗancan bauɗaɗun buzayen sukeyi, shiru har  dare har wayewar gari bai fito ba har rana ta kuma ɗagawa hankalin Mom yaƙi kwanciya ta tashi ta nufi ɗakin nasa ta buɗe ta shiga tare da isa gadon da sauri tace “Nuraddeen kashe kanka zakayi akan mace haba Deen Meye yake damunka da zaka kwanta a ɗaki kayita rawar sanyi" cikin ciccijewar murya yace “Mom..... Mutuwa zanyi...." Da sauri ta haura gadon tana danna masa ƙirji tace “Ka rufamin asiri Deen wlh bazaka mutu akan mace ba ka kwantar da hankalinka nayi maka alƙawarin indai nice mahaifiyarka sai sama maka wadda tafita" cikin azabar ciwo yace “bazan samuba Mom please"

Yanda jikinsa yake rawa yasata kiran likita yayi treatment ɗinsa Dad ya shigo ɗakin ya miƙa

mata waya yace “Tun ɗazu Junior yake kiran wayarki" karawa tayi a kunnenta tace “Babana ya Austaralian?" Cikin mutuwar jiki yace “Not Lucky Mom still banganta ba ance tana Cairns duk inda nake tunanin zan iya samunta naje babu wani bayani Mom inajin tsoron wani abu ya faru da ita" Hamm ta sauke ajiyar zuciya itakam tana ganin jarabawa duk akan mata ƴaƴanta suke neman zaucewa.
Ƙwallar idanunta ta share tace “Indai ana nema za'a dace Junior ƙaddararku ce nidai banji a raina Batul ta mutu ba ta ɓuya ne saboda tsoron sake maimaituwar abinda ya faru a baya Insha Allahu soon zata bayyana gareka" lumshe idanunsa yayi tare da kwantar da kansa saman pillow yace “Kuma zata soni Mom tun kusan sati ɗaya gabana yake faɗuwa" murmushi tayi tace “Bazata taɓa daina sonka ba" ajiyar zuciya yayi yace “Yaushe Bobbo zai dawo?" Kallon Deen tayi tace “Shima yana kwance ciwon soyayya ne yake damunsa yanason wata buzuwar yarinya da suka haɗu anan Austaralian Su Dad ɗinku da Shaikh Muhammad Saleem sunje nema masa aurenta iyayenta sun wulaƙantasu sunce bazasu bawa bare aurenta ba, shine yake kwance tun jiya babu ci babu sha gashi ma suna shirin auradda ita.

Murmushi yayi ajiye wayar tare da shafa sumarsa ya zubawa ƙaton hoton Batul idanu dake ajiye a duk wani guri da yake zama hatta office na ma'aikatun da yake jagoranta kowanne sai ya saƙala wannan hoto.
Juyawa yayi ya kafama hoton idanu yana mayar mata da martanin Murmushinta yace “Nayi mafarkin kina rayuwa dani a zuciyarki Bea ki dawo mu gyara rayuwarmu muyiwa Jany gata nasan yanzu tanason ganin Dad ɗinta Batul ke rayuwata ce"
Tashi yayi ya fara goge hoton tare da kissing lips ɗinta yace “Bakisan komai game da mijinki ba nasan zaki karemin kanki ki adanamin daɗina ko?" Dariya yayiwa kansa tare da shafa kwantacciyar sumarsa yace “Soon zan baki ƙanin Jany naga kina tashi daƙyar na tsokaneki muyita zagaya compound na gidanmu kinaso ko?"...............

*Paid book 500 VIP 1k via 9031307566 Fauziyya Tasiu Umar Opay*

*Contact me*
*09013718241*
[7/9, 11:02 AM] Oum Hairan: *SIGNED MARRIAGE*
*_(Kalma ɗaya)_*

*Oum Hairan*

*____________________________________*
*Book 2 page 17-18*
*____________________________________*

Komawa yayi ya kwanta tare da buɗe wani hotonsu da yayi musu ranar darensu na farko bayan komai ya kammala lokacin da Dad ya kirasa yake masa hannunka me sanda akanta ashe shima rayuwar farin cikinsa yake nema, sosai yayiwa Allah gdy lokacin da ya samu labarin abinda ya faru a ƙungiya lokacin da  Daddynsa yayi ƙoƙarin haikewa daɗinsa ashe zata iya kare kanta itama? Murmushi yayi tare da ɗaukar cup ɗin Wine ɗin dake samen bedset ya kurɓa ya ajiye tare da yamutsa sumarsa cikin shekaru biyun abubuwa da yawa sun faru shi kansa karfin addu'ar mahaifiyarsa ce da kuma nisan kwana ya kawosa wannan lokacin.
Sake zubawa hoton idanu yayi as emerging ace yanzu ne suke cikin wannan rayuwar yasan zasu rayu cikin kwanciyar hankali, babu wani tarnaƙi da zai shigo rayuwarsu bare ya hana musu farin ciki.
Lumshe idanunsa yayi tare da ɗaukar wayarsa ya fara kiran layin Batul na Nigeria ya kira sau ba adadi baya shiga kamar ko yaushe sake yamutsa sumarsa yayi ya tashi zuciyarsa nayi masa zafi ya zubawa ƙasan gidan nasa idanu yana kallon ɗaiɗaikun mutanen da suke kai kawo ya busar da iska me zafi tsayin lokaci zuciyarsa har nauyi takeyi masa kullum tsammani yakeyi na ganinta bai rabo da Melbourne a tunaninsa ko nan ta koma da zama shine har Sydney but kullum amsar tasa shiru ce ya gaji da yawo tsakanin ƙasashe zuciyarsa kullum tana faɗa masa Bea ɗinsa tana kusa dashi to amma mene yasa ta kasa nemansa?

Lumshe idanunsa yayi ya kwantar saman  garun yace “Dole zata nemeni to ta ina?" Buɗe idanunsa ya sakeyi, lokacin da yace mata gashinan zuwa Australia Bayan ya shigo Austaralia a hanyarsa ta zuwa gidan da yake tunanin Lateef zai yi camping nata komai ya faru da ya zamo silar ɓacewa junansu gashi yanzu komai ya wucce ya zama tarihi babyn da suke burin hallakawa wadda ta dalilinsa suke son su jefata a ƙungiyar asiri, yau tanada shekara kusan biyu a duniya.
Yanajin duk wani motsin gudan jininsa a cikin nasa jinin yana rayuwa da kewarsu kullum da wannan damuwar yake kwana a mafi yawan darare takan hanashi bacci, yana tsoron halin da zai riske Batul a ciki duk da cewa baya zargin faruwar wani abu domin kuwa masifar da aka

ɗora mata ta feeling kafin mutuwar Lateef ya sanar dashi ya karyata wannan ma shine dalilin da yasa ƙungiya tayi Allah wadarai dashi tare da janye masa tallafi a ƙarshe suka bayar da jininsa ga dodon tsafi wannan ya faru ne ranar da Batul ta haifi Jany ranar ne duk wani ƙulli da aka shafe shekara sama da 30 ana kullawa ya rushe, ranar ne alƙaluman tsafi suka ƙwacewa dukkan wani wanda ya dogara da kungiyar Emenisty ranar ne kuma ruhika suka rabu da gangar jiki da yawa, still dai a ranar ne asirin ɓoye ya fito fili haka dai a ranar ne jinin wasu manyan hadiman ƙungiya ya halarta ga dodon tsafi ciki harda Daddy da Lateef da shi kansa Ma'eesh ɗin, a wannan rana ne  a gaban idanunsa akayiwa Amininsa a farko maƙiyinsa a ƙarshe Lateef dandatse aka cire  gabansa da marainansa aka gasawa wasu manyan jakadun ƙunguya a cewarsu saboda jin daɗin kansa da burarsa ya rusa musu shirinsu na shekara sama da 30 shi kuwa Dad tik sukayi masa suka jorner masa wani abunsu na tsafi ya rinƙa zuƙe jini da ruwan jikinsa Saida ya ƙafar dashi ƙaf sannan ya faɗi matacce.

A lokacin da suka juyo gareshi ne suka nemeshi suka rasa gashi shi kuma a gurin yana kallonsu duk yanda sukaso ganinshi ta cikin madubin tsafinsu ya gaza nuna masu shi and end ma idan suka cika binciken madubin tarwatsewa yakeyi ko kuma wanda ya dage wajen gano shi ta cikin madubin kawai aji ya saki ƙara ya faɗi matacce, a wannan halin Saida ya kwana uku babu ci babu sha gashi a ɗaure shidai baisan ya akayi ba kawai ya wayi gari ya ganshi a kwance a wani ɗaki ya buɗe idanunsa yana ƙarewa ɗakin kallo can yaga wani mutum ɗaure da wani abu me kama da ganye a gabansa irin dai shigar nan ta arnan daji shidai daga haka ya kuma fita daga hayyaci ya kuma farkawa ne ya gansa a gefen titi a tashe mutane sun zagayeshi daƙyar cikin tambayoyin da ake ta yi masa ya iya amsar wayar wani yasa number  Mijin mahaifiyarsa, daganan Saida ya shafe wata shida baisan komai dake faruwa dashi ba a duniya yake a lahira yake oho.
Bayan watanni shida ne ya farka cikin wani gigitaccen yanayi Allah yasa ƙaninsa Bobbo da Mijin mahaifiyarsa Alh Hakeem suna tare dashi suka rirriƙeshi tare da fara tofa masa duk addu'ar da suka san zata zama waraka gareshi kusan awa guda sannan ya dawo hayyaci ya sauke idanunsa kan Mahaifiyarsa yace “Kin ganta can tana kallo na nace tazo taƙi zuwa Mom ki faɗa mata ba raayina ne yasani zama cikin matsafa ba gadarmin kukayi Mom ki faɗa mata itan haske ce ga rayuwata itan itace ƙaddarata kar ta gujeni Ni ɗim don ita kaɗai aka halicceni Mom Batul tanason rabani da Ƴata idan ita ta gujeni ta bani ƴata....."

Rufe masa baki tayi ta kalle Abbuh Hakeem tace “Har yanzu yaron nan bai dawo hayyaci aci

gaba da basa kulawa" jinjina kai yayi Bobbo yace “Mom a ƙara sauke masa Kur'ani zai samu relief sosai sun rikita masa ƙwaƙwalwa ne ta yanda bazai iya tuna komai ba but anyi nasara tunda ya farka da hoton Budurwarsa da ɗiyarsa akwai yiwuwar komai ma zai dawo masa a ƙwaƙwalwa saidai kuma dole ne sai an saka tsaro akansa fah kinsan bai saba zaman guri ɗaya ba, nasan zuwa yanzu sunsan bai mutu ba kuma zasuci gaba da bibiyar sa don ganin bayansa kamar yanda sukaga bayan Lateef da Daddyn Junior"
Jinjina kai tayi tana share hawaye duk ita ta jawa ɗanta shiga wannan masifar daga bijirewa maganar iyaye taje ta jefa kanta a masifa shima ta jefashi gashi ya cinye rabin rayuwarsa bai amfana da komai ba sai kaico da kaucewa tafarkin addinin Muslunci kullum kokawa suke ita da mahaifinsa akan ganin yabi addinin kowanne ita tayi nasarar jansa zuwa musulunci amma kuma Daddy ya juya mata tunanin yaro da tsari na addininsu na yahudanci yanzu ita ina zasu fara neman Batul tana tsoron kar taje tayi aure kan aure, koda yake abin zai zama me sauki tunda a cikin Musulunci suke dukkansu to amma shima auren yarjejeniyar da sukayi ita da Ma'eesh ɗin yanada asali a Addinin yahudanci tunda shidai ta fahimci addini biyu yake bi abinda yayi masa daɗi a Addinin Musulunci shi yakeyi addinin Ubansa ma yahudanci zaɓa yake daga ciki ya ɗauki wanda yayi masa daɗi.

Sosai aka dage masa da magungunan Islama ƙarshe ma gidan Shaikh Muhammad Saleem ya koma da zama inda basu barshi ya ƙara fita daga ƙasar ba Saida suka tabbatar da samun lafiyarsa, tashin farko Kano yaje inda ya samu mugun labarin Inna ta Saida gidanta ta koma Lagos koda ya koma Lagos ya gama bulayinsa bai ganta ba haka ya ɗauki hanyar Austaralia inda kai tsaye Melbourne ya sauka ya nufi gidan Daddy wanda akayi camping na Batul a ciki abun mamaki dukkan komai na gidan ya daskare ya zama gunki hatta mutanen dake hidima a gidan dukkansu sun zama kwarangwal domin an tsafacesu ne ta yanda bazasu iya guduwa ba. Shidai zuciyarsa na rawa haka ya shiga gidan ya fara Ratsa faluka da ɗakuna har ya kai ɗakin ƙarshe na gidan inda anan aka ajiye Batul ya shiga ya fara bincikensa abu biyu ya samu a ɗakin daga wayarta sai zoben diamond daya sanya mata daren da zai tafi South Africa ɗauka yayi yana juya zoben a hannunsa kafin ya ɗauki wata takarda da ya gani a yashe a ƙasa cikin wani bushasshen jini sai yanzu ya lura da tarin Glass ɗin dake ɗakin da kuma kwarangwal ɗin dake kwance cikin ƙura da jini bushasshe, haskawa yayi sosai tsutsa duk ta gama cinye mutumin dake kwance mace ce ko namiji bai sani ba daƙyar cikin tashin hankali ya ɗauki takardar rubutune akayisa da rashanci da jini.

“Zaka Sameta a duniya ne bayan ruhina ya mutu soon Matarka tana Cairns ta kashe gangar jikina amma ruhina zaici gaba da bibiyarta har sai na cika burina, nasan zakazo bayan ta haihu

an kashe gangar jikina ta biyu a gabanka......"
A tsorace ya rinƙa kallon kwarangwal ɗin tare da ja da baya ganin yana wani irin motsi tare da wata irin curewa waje guda wannan bushasshen jinin ya zama ɗanye ya rinƙa haɗewa yana curewa ƙarshe ya zama kamar ƙwai wannan kwarangwal ɗin ya ɗauka ya maƙala a zuciyarsa take saiga wata hallita ta tashi tana ƙyalƙyala dariya ta cafki wuyansa tana ƙoƙarin kashe shi cikin wata murya wannan dodon ya fara cewa “Ma'eesh jiran zuwanka mukeyi dama munsan dole zaka biyo Matarka da ɗiyarka hahaha dole mu shanye jininka tunda ka hanamu na Matarka da ƴarka sai mun kasheka! Hhhhhh sai mun kasheka..... Jini.....zansha jini..... Hhhhhh jinin ɗana zansha....."

Cikin fitar hayyaci ya rintse idanunsa ya fara karanto wata addu'a da Muhammad Saleem ya bashi yace saboda tsaro domin har yanzu ana biyar rayuwarsa waɗancan matsafan da aka sadaukarwa dashi tun yana cikin uwarsa sunanan sun sake shiri a kansa, addu'a yakeyi sosai yana riƙe maƙogwaronsa inda daga baya yaji an saki wata ƙara an sakeshi wuta ta kama ɗakin ganga ganga take yaji wani hucin zafi yana neman narkar dashi haka ya fita a guje daga gidan da ashe gabaɗayansa ne ya kama da wuta yana fita ya nufi tashar jirgin ƙasa ya shiga na Sydney Saida yayi sati biyu yana karɓar magani sannan ya fara fita inda a sati na uku ya nufi Garin da yafi rayuwa inda ya baza kasuwancinsa da duk wasu halattatun kuɗaɗe dake hannunsa wato Cairns garinsa na haihuwa kenan nan ne state origin nasa domin shi ba haifaffen Rasha bane kuma ba haifaffen Sudan bane, lokacin da dangin Mom suka koreta bayan tsira daga kaidin  Dad da yayi masu ƙaryar musulunci ya nemi aurenta iyayen sukaƙi ita kuma ta kafe saishi ƙarshe sukaje aka ɗaura musu aure  batare da amincewar iyayenta ba ya ɗauketa ya tafi da ita Rasha.
To bayan iyayenta sun koreta sunce bazasu raini ɗanta na shege ba Shine ta yanke shawarar barin yankin gabaɗaya nan zuciya ta raya mata ta tafi Austaralia, acan ta samu  wani gidan abinci ta fara da wanke wanke da shara bayan ta haihu ne kuma ta samu miji ɗan kasarta ne ta Sudan mazaunin Austaralian ɗan kasuwa sukayi aure dashi anan ne kuma ta haifi  Nuraddeen sannan Nuwairah da Muhsin ta haɗa kan yaranta huɗu harda Ma'eesh wanda yanada shekara biyar ne Mahaifinsa ya gano inda take yaje ya sace ɗansa a lokacin mijinta ya gina mata katafaren gurin cin abinci  na yan Africa a ƙasar Austaralia, a haka suka raineshi idan Nazhan ya sace shi sai ya ɗauki shekaru baya tare da ita, haka itama idan ta samu dama ta sace shi sai ta ɓatar dashi ta tura shi Nigeria gidan yayanta Muhammad Saleem don ya samu ilimin addini, shidai a haka ya girma tsakanin ƙarya da gaskiya.
Ajiyar zuciya ya sauke tare da kai idanunsa ga agogon da yake maƙale jikin bangon wajen hutawar 2:30am ya sake sauke ajiyar zuciya ya nufi dakin baccinsa ya sake wanka yayi alwala ya tayar da sallar nafila zuwa yanzu so yake ya koyi miƙa Komansa ga Allah tare da neman mafita a gareshi kamar yanda Mom take sanar dashi kullum  ya jima yana kaiwa Allah kokensa kamar yanda kullum Mom Abbuh da Shaikh Saleem suke faɗa masa da ɗan uwansa Nuraddeen, bai koma ya kwanta ba Saida yayi sallar asuba kasancewar unguwar tasu babu musulmi sosai a gida yake Sallah bayan ya idar ne ya kwanta bacci ya ɗaukeshi kamar kullum

dai mafarkinsa na Abar ƙaunarsa ne saidai yau yanayin damuwa ya riƙeta a ciki abinda ya sanya shi yana tashi ya fita ya nufi ɗaya cikin gidajen abincinsa sadaka yakeson yi domin fatan duk masifar da zata shigo rayuwar masoyiyar da ɗiyarsa tazo musu da sauƙi umarni ya bayar na cewa yau duk wanda yaci abinci a gidajen abincin nasa kar a karɓi kuɗinsa sannan ya nufi babban Companynsu na drinks ya zauna a office ɗin ba tare da iya hassala komi ba, ganin hakan bai masa bane ya kuma fita ya nufi asibitin da yake aiki, haka yake yini yawo tsakanin masa'antun nasu ba tare da ya iya taɓuka komi ba"...........

*Paid book 500 VIP 1k via 9031307566 Fauziyya Tasiu Umar Opay.*

*Contact me*
*09013718241*

*OUM HAIRAN*
[7/9, 8:31 PM] Oum Hairan: *SIGNED MARRIAGE*
*_(Kalma ɗaya)_*

*Oum Hairan*

*____________________________________*
*Book 2 page 19-20*
__________________________*__________*

Fasalta irin tashin hankalin da Batul ta shiga lokacin da labarin irin wulaƙancin da su Baffa Maigari sukayiwa iyayen Deen wannan ma ɓata baki ne tayi kuka kamar ranta zai fita a ƙarshe taja bakinta tayi shiru iya Samha ce tasan shirinsu, haka ake ta shirye shiryen biki bata cewa kowa komai Samha ce ta sanar da Inna Laure zataje Niamey akwai ƙanwar babarta zata kai mata katin biki kuma zata iya kwana biyu a can, ba tare da tunanin komai ba tace "Ai kuwa badan kar na ɗora Miki nauyi ba da na baki wasu yan kuɗaɗe kinyo mana siyayya kinga babu abinda aka siyo har yanzu" satar kallon Batul Samha tayi tace "To Inna mu tafi tare mana dama Nima nayi tunanin hakan in yaso saita zaɓo irin abubuwan da take so Kinga lokaci sai ƙurewa yake yi saura kwana takwas fah ɗaurin aure"

Ba tare da tunanin komai ba Inna ta zuge jaka ta zaro kuɗi zata basu Samha tace Inna kibar kuɗin nan idan Batul ta tafi ɗakinta sai kija jari mu muna da kuɗin da idan dukka auren zamu ɗauki nauyi na bazamu girgiza ba"
Yarda Inna tayi suka shirya Samha tace "Inna bari mu tafi da yaran nan saboda kar su dameki da ƙiriniya suma mayi musu siyayyar kayan fitar biki" cewa tayi "Eh fah Waɗannan koɗaɗɗun ƴaƴan naku sai ku ai kuje da abinku inba haka ba magana ma ta isheni a garin nan" sudai suna samu suka fice kai tsaye daga Damagaran motar Katsina suka shiga basu suka shiga Katsina ba sai dare suka nemi hotel suka kama bayan sun shiga ɗakin hotel ɗin ne suka kalli juna Samha tayi dariya tace "In sun san wata ai basusan wata ba kulle wayarki tun a nan bamu sake kunna MTN line sai mun keta hazo yanda duk nacin me naci bazai iya biyomu ba"

Zama Batul tayi dafe da kai tace "Allah sarki Inna yanzu nasan kanta zatayi wabi cewa zasuyi ita ce tasani na gudu Ni kuwa wlh dana auri Anwar gara na kare rayuwata a ɗebe kwanukan MB kitchen's dariya sosai Samha tayi tace "Kedai kawai kina son rayuwa da Deen kinga haɗaɗɗen Guy ɗan ƙwalisa ana shirin manna Miki wani garan ƙauye koda yake Anwar bashida laifi kawai dai wayewarmu ce ta girmi tunaninsa, sai wani ihu suke a France yake yo inda France tana cikin wayayyun ƙasashe meyesa su basu waye ba, nifa wlh na matsu naga lifestyle naku da Deen nasan za'a ɗauki darasi"
Murmushi tayi tace "Hmmm bakiga lifestyle ba tunda bakiga rayuwarmu da Ma'eesh ba Samha Bama gajiya da cinye juna fah gashi da zaƙi nifa badan kar nayi ƙarya ba zan iya cewa Yafi zuma daɗi"
"Ma'eesh! Ma'eesh!! Nikam kamar nasan wannan sunan Batul? Ohhhh Manager na MB kitchen's sunansa kenan yanzu daganan ina mukayi?" Taɓe baki tayi tace "Muje Kano muga gidan da aka siya daganan mu koma Abuja idan so mu ɗaga ko me kikace?" Jinjina kai tayi tace "shikenan hakan za'ayi" wanka sukayi sukayiwa ƴaƴansu sukayi sallah suka kwanta bacci.
Kiran Deen ne ya shigo tana ɗagawa tace masa "Ka koma ne? Murmushi yayi yace "Jiya naji damar jikina yau na sauka a Austaralia course Yayana bashida Ify shima but ya fara jin sauƙi, ya shirye shiryen biki?"

Murmushi tayi tace "Nima ina hanya cikin satin nan" zaro ido yayi yace "Ya batun bikin naki?" Murmushi ta sakeyi tace masa "Bazan cuci kaina bane Noor tunda sun hanamu aure to Nima wlh bazan auri wanda sukeso ba su barni na rayu da ƙaddarata" ajiyar zuciya yayi yace "Idan kikazo sai musan abinda ya dace kawai muje Embassy a ɗaura mana aure tunda parents ɗinki sunƙi ɗaura mana" dariya sosai abin ya bata yace "Haba Deen abin na kaɗo ai ba hauka bane

nayi Sign married sannan yanzu nazo nayi Embassy married ai kayimin faɗan nabi komai a hankali, tunda dai komai lokaci ne"
Kwantar da kai yayi yana kallon Ma'eesh dake gefensa yace “Nace da Bro Wife ɗina a ɗaya cikin Restaurants nasa take aiki idan kin dawo zamuje mu gaisheshi yasa mana albarka, ko na haɗaku ku gaisa?" Saurin girgiza kai tayi tace “Aa ka bari dai nazo sai muje mu gaisheshi ai yayanmu ne bai kamata ayi masa gaisuwar miƙe ba" Murmushi yayi yace “Hakane kinyi gsky yanzu yaushe zaku taho?" Haka sukayita hirarsu tare dayi musu alƙawarin zai sama musu visa urgent, haka kuwa akayi kwana biyun da sukayi a Kano sunga gidan da Batul ta siyawa inna gidane me kyau ya ƙawatu duk da ba wani babba bane Saida ta zubanta komai na amfani hatta kayan abinci sannan ta bawa Janah kuɗi masu yawa tace taje ta ɗaukota ta dawo da ita nan" washegari kuwa Zakara ya basu Sa'a sai Cairns shigar dare sukayi shigar dare sukayi sosai domin Saida suka yada zango a Canada sannan suka ɗauki hanyar Austaralia.

Dake Turai ba Africa bace a daren suka dangana da gida domin kuwa a airport ɗin suka ishe Deen yana jiransu kallo daya tayi masa ta tabbatar da ramarsa sosai ya bata tausayi ta kwantar da kanta a jikinsa tace “My Noor ka rame da yawa don Allah kar ka sanya damuwa a ranka komai yanada lokaci" shafa kuncinta yayi yace “Bazasu gane bane Fateemah inashan wahala fah ina buƙatar abokiyar rayuwa wlh" murmushi tayi a ranta tace “Gara ma kai baka ɗanɗana ba but a zahiri ce masa tayi lokaci zai zo soon Insha Allahu.
Saukesu yayi bayan sun biya ta Restaurant nasu sun karɓi abinci a ƙaramin office ya tadda Ma'eesh yana zaune ya zuba uban tagumi ya taɓashi yace “Har yanzu bazaka rage damuwar nan ba Bro no condition is permanent please ka rage damuwa ko dan Ifyrka" kifa wayar yayi a ƙirjinsa tare da danna sweetch ɗinta ya zubawa ƙaninsa nasa  idanu yayi yace “Ka ɗaukosu ne?" Jinjina kai yayi yace “Abinci ma muka biyo su karɓa sai su wucce gida Bro na mutu akan Babyn nan Teemah ta haɗu sosai rayuwa ta ce?" Murmushi yayi yace “Allah yasa rabonka ce Deen Kaje ka kaisu gida dare yayi Ba zamu haɗu a wannan karon ba Ni gobe zan koma Sudan banason mutuwa a garin nan gara naje na mutu a gaban Mom ta dafa kaina tayimin addu'a Inason bata duk wani abu dana mallaka idan na mutu ta nemi Batul ta batashi ita da babynmu su rayu rayuwa me inganci"

Miƙewa yayi ya fice in da sabo ya saba da Waɗannan kalaman na yayan nasa kullum abinda yake cewa kenan matarsa da ɗiyarsa shi ya fara sarewa yanda ya baza ma'aikata ake neman yarinyar nan inda tana raye da tuni an ganota" jan motar yayi ya kaisu gida sukayi masa godiya

suka shiga ɗakinsu kawai suka gyara sukayi sallolinsu suka kwanta baccin gajiya sun fara mantawa da sanyin Austaralia gashi sun dawo lokacin saukar Snow abin ba sauƙi haka suka sa shirga shirgan kayan sanyi suka kwanta bacci kuwa ya sacesu cikin dare ta farka a firgice tana furta “Innanillahi wa innah ilaihirraji'un!" Abinda ya tashi Samha tace “Ya akayi?" Ajiyar zuciya tayi tace “Na godewa Allah daya zama mafarki Samha kwanan nan Ma'eesh ne ya dawo a mafarki na, na fara cire shi a raina har ina jin a raina fah ko bayyana yayi gareni bazan iya sake rayuwa dashi ba saboda hankalina bazai kwanta ba za ma da matsafi" tsaki Samha tayi tace “Wlh da kayan haushi kike yanzu yaushe zaki koma aiki yanzu nake gani gobe Shugaba yana neman dukkan ma'aikata zai yi taro dasu zai koma ƙasarsa shan magani" taɓe baki tayi tace “Gsky gobe ba zanje ba zan huta shi kuma Allah ya bashi lfy"
Komawa sukayi suka kwanta da safe Samha ta tafi aiki ita kam zamanta tayi a gida da yamma Deen yazo yake ce mata Bro yakai airport nan suka shantake da hirarsu ta masoya.

Haka rayuwa taci gaba da tafiya ta kowanne ɓangare babu daɗi Inna ta fuskanci ƙalubale daga ƙarshe ne Alh Khamilu yazo ta zayyane masa komai Aikuwa ya rufe yan uwan nasa da faɗa yace sunci amanar maraici Meyesa yarinya zata kawo wanda takeso suƙi bashi su haɗata da wanda bataso, yanzu in a baya sunce laifin uwarta ne yanzu kuma na waye? Waye yake da alhakin sake fantsamarta duniya?" Dake yanada citta a hannunsa take sukayi nadama suka bashi haƙuri duk kuwa da cewa shi ce masa sukayi batada manemi ne shiyasa sukeson haɗata da ɗan uwanta, da kansa yaje ya bawa Inna Laure haƙuri yayi mata jagora har Kano inda suka samu lambar Batul gurin Janah bai bar sabon gidan Inna ba Saida ya kira Batul lokacin tana gurin aiki ta ɗaga suka gaisa yace “Batula baki ganeni ba ko? To ubanki ne Khamilu" cike da kunya tace “Lahhh Baffa ina yini ya gida da mutan gidan?" Dariya yayi yace “Kinci uwaki ƴar ƙaniya to ki turomin number surukin nawa sai jiya nake sanin abinda ya faru wlh banga laifinki ba Batula Ni daɗi ma naji da kika nuna musu kin san kanki ke kam yanzu idan ba'a rarrasheki ba ai ba'ayi Miki dole ba"
Cikin kunya tace “To Baffa na gode" tana aje wayar ta tura masa number Deen tayi wani tsalle ta rungume Samha tace “Ke burinmu ya kusa cika yanzu baban Anwar ya kirani yace na tura masa number Deen nasan maganar aurenmu za'ayi wlh na gaji da haɗiyar ƙwayar kashe sha'awa nima Gara naje na warwasa na baje masa ya lasa ya tsotsa yaci ya ƙoshi" dariya sukayi tare da tafawa suka kama rawarsu ta yan Iskan gari, ranar basu bari sun tashi ba gida suka koma harda haɗa ƙwaryan party Suda ƙawayensu tun basusan me ke faruwa ba.
Da dare kuwa kiran Inna ya isheta ta ɗaga suka gaisa tace “Yanzu sai yaushe zaki dawo a yau ɗinnan Ƙanin Mamar saurayinki yazo sun kawo dukiyar aure da sadaki Miliyan biyar an tsayar da ranar aure wata guda me zuwa".......

*Paid book 500 VIP 1k via 9031307566 Fauziyya Tasiu Umar Opay*

*Contact me*
*09013718241*

*OUM HAIRAN*
[7/10, 11:18 AM] Oum Hairan: SIGNED MARRIAGE
*_(Kalma ɗaya)_*

*Oum Hairan*

*___________________________________*
*Book 2 page 21-22*
*___________________________________*

Wata alkafura tayi ta tashi a gadon tace “Inna 5Ml saidani zaki kumayi?" Dariya abin yaba Inna Laure tace “Ba saidaki zanyi ba Batool abinda suka kawo kenan sunce saboda yanayin faɗuwar Naira abubuwa sunyi tsada kuma irin wannan auren ba shiryawa akayi ba dole sai jin ƙai ya shiga, yanzu dai yaushe zaki dawo Kano?" Ajiyar zuciya tayi Samha ta karɓe wayar tace “Inna mu bari sai bikin ya rage saura sati biyu inaga Zaifi" a haka suka bar abin sukaci gaba da shirye-shiryensu sabon babi na soyayya ya buɗe tsakanin Batul da Deen ko yaushe suna manne a waya ko suna chat kasancewar tun kwana biyu da sa ranar bikin ya tafi Nigeria da yake anan yake ra'ayin zama a Abuja yanata gyare-gyaren gidan da zasu zauna ranar da zasu tafi ne wani abu me kama da almara ya faru suna zaune a reception suna jiran cikar lokaci wani ƙamshin turare da bazai taɓa ɓacewa a ƙwaƙwalwarta ba ya ziyarceta abinda ya katse mata numfashi na tsayin daƙiƙu ta miƙe zumbur tare da fara dube² ajiyar zuciya tayi ta koma ta zauna tare da dafe kanta.
Samha dake kallonta ta dafa kafaɗarta tace “Me kike nema?" Ajiyar zuciya tayi tace “Babu komai" janye hannunta tayi tunda tace babu komi tasan bazata mata bane, da wannan aka fara kiran matafiya suka tashi suka shiga jirgi bayan kowa ya gama zama jirgi ya tashi bakin Batool ɗauke da addu'ar neman kariyar Ubangiji, har yanzu kuma hancinta bai daina jiyo mata ƙamshin daddaɗan turaren da ta gaza jinsa a gurin kowa sai a gurinsa shi kaɗai wato Ma'eesh inda

taketa satar kallon gefe da gefenta amma bataga wata alama da take nuna akwaishi a gurin ba. Ba su so tafiyar tazo musu a karkatse ba but dole haka suka haƙura ashe jirgin yawo suka biyo Saida suka tsaya a Japan suka kwana biyu abinda yake ƙara bata mamaki kuma ya koma tsoratata yanda wannan ƙamshin turaren yake bibiyarta idan ta duba kuma taga babu kowa.

Daganan suka tashi sai Canada daga Canada suka dira a birnin tarayya suka kwana ɗaya abinda ya bata mamaki duk kiran da takewa Deen wayarsa bata shiga daga ƙarshe aka turo mata saƙo.
“Kiyi haƙuri na turo Muhsin zai ɗaukeku zuwa Kano Nima zan biyo bayanku Fateemah ina ɗakin taro ne" Jinjina kai tayi babu ɓata lokaci batare da tambayar address ba saiga wani saƙon ya kuma cewa “Zai kiraki ƙaninmu ne zama kiga kama" tana gama karanta daƙon kira ya shigo wayarta ta ɗaga “Sosai gabanta ya faɗi jin Muryar tasa, yace “Auntyna ina jiran ku" saurin sauke wayar tayi a kunnenta tace “Nikam na shiga uku Samha komai nashi yake zamemin, meye haɗin ƙanin Deen da Muryar Daddyn Jany?" Murmushi Samha tayi tace “Wannan mayen mutumin zai kashe Miki aure idan bakiyi da gaske ba, yoni na taɓa ganin wannan masifa kin damu da mutumin da neman sanin yanda kike da lafiyar ɗiyarsa dake hannunki ma ya gagareshi"
Iska ta furzar tace “Inashan wahala da Zuciyata akansa Samha kema kin kasa fahimta ta wlh na faɗa Miki a yanzu ko bayyanarmin yayi bazan ɗaukeshi nabar Deen ba but kinsan meye yanzu yake zuwa raina? Shin daga shekara biyun yarjejeniyar ta ƙare kenan?" Tsaki Samha taja tace “Wai yarjejeniya toke ubanwa yace Miki aure kukayi kawai kunyi iskancinku ne amma ko a kafirci aure a curch ake ɗaurashi bare a musulunci da sai anyi siga waliyyay sun haɗu an bada sadaki shaidu sun shaida sannan aure ya ɗauru"

Bata kuma cewa komai ba suka isa jikin motar ta Zubawa Muhsin ido da yayi caraf ya cafe Jany yana cillata yana dariya dimple ɗinsa na lotsawa hatta dariyarsa irin ta Ma'eesh ce hasken tsananin kamar har ta zarce misali hasken fatar sa ne kawai ba irin na Ma'eesh ba shi nasa da sirkin duhu a ciki saɓanin Ma'eesh da yake tar irin hasken Turawa har wani ɗaukar idanu yakeyi. Juyowa yayi yana kama hannun Jalal ya rusuna yace “Gaisuwar ban girma matar Babban Yaya Uwar sha lelen Mom!" Zuba masa idanu tayi ya buɗe musu motar suka shiga ya lura da kallon ƙurullar da take yi masa but yasan dalilinta domin kaf gidansu babu wanda suke kama ta Kwabo da Kwabo irin shi da Mijinta duk kuwa da cewa Uwa suka haɗa koda yake dukka da Mommy suke kama dama Deen da Aunty Nuwairah ne suke basuyi kama dasu sak ba

su sunfi kama da Abbuh Hakeem amma a hakan akwai wasu yanayiyyika da suma ake cewa suna kama da Mom, jan motar yayi a guje kiɗansu na Sudanies na tashi a motar ita kanta motar ƙamshin turaren da yake rikita mata lissafi takeyi, Samha sai magana takeyi mata ita kuwa kanta ya kulle sai juya mata yake yi musamman da take jiyo hirarsu da Jany, yarinyar tana masa surutu shima ya dage sai tayata yakeyi yana ce mata "Babyna yau taga Dad ɗinta, kina cikin alkhairi yarinya"
Nisa na tsakanin Kano da Abuja ita dai Batool sai ji tayi yana cewa da ita "Matar Big bro ko baki gaji bane mu juya?" Firgigit tayi ta dawo hayyaci ta dauki jakarta ta fito ta nufi gidan ya ɗaga murya yace "Am Matar Big bro sai nazo ɗaukar amaryata" cije lips ɗinta tayi ta nufi cikin gidan tana ayyana ya fahimci halin da ta shiga da ganinsa ma shine yasa yake neman zautata.

Duk yawan mutanen dake tsakar gidan na Inna bata iya kula kowa ba ta shige ɗaki ta fincike mayafin kanta ta wullar tare da zubewa kan gadon tana furta "Innanillahi wa innah ilaihirraji'un Allahumma ajirni fi musibati wa'akalifni khairin Minha!" Jin yanda lazumin "hasbunallahu wa ni'imal wakil" ne yasa Samha zubanta ido tace "Na lura da rikicewarki tun fitowarmu da kikayi arba da wannan kyakkyawan guy ɗin, ya hayyu ya ƙayyumu Teemah An ƙure kyau a wajen nan nifa Saida nace to wai samarin aljanna sun fara kawo mana ziyara duniya ne?"
Miƙewa tayi tace "Kinsan me ya bani mamaki? Samha bayan Muryarsa da yanayin dariyarsa da kuma kama ta zahiri dana gani hatta tsayinsa da faɗinsa irin nasa ne, Jany bata kama dani but daya ɗauke kasa bambamce bambancin tsakaninsu nayi, kince Jany tana ɗiban kama da Deen shi kuma wannan me Jany takeyi dashi?" Kama hannunta Samha tayi tace "Ba kama bace gaurayar jini ce, wallahi azza wa jallah badon nasan komai game da Jany ba babu yanda zaayi naga mutumin nan ɗauke da Jany naki bada shaidar shine ubanta, saidai karki manta duniya tanada faɗi kuma dukkanmu Allah ɗaya ne ya haliccemu sannan inaso ki rinƙa tuna abu guda ɗaya nasabar gari ɗaya ma tana bin jini, Batool kince Kakar Jany ammana mahaifiyar Daddynta itama Sudanese ce kuma kince Ma'eesh da mahaifiyarsa yake kama Kinga kenan maybe ko sun haɗa wata alaƙa ta jini ta nesa ma bata kusa ba, wannan dai ƙanin angonki me jiran gado ne nan da 10 days Kinga kenan bashida alaƙa da Ex-husb ɗinki a cewarki"

Komawa tayi ta zauna tana sake dage kanta tace "Idan ko ya zama haka maganar gaskiya zan sanar da Deen banason wannan ƙanin nasa a sashina saboda zai rinƙa firgitani Samha Ni kaɗai nasan me nake gani a tare da yaron nan kuma na fahimci ya gane yanda na ruɗe da ganinsa har wani zolayata yake yi" dariya Samha tayi tace "Wannan ango yana ganin rayuwa tun yanzu za'a fara kafa masa dokar wanda zaizo da wanda bazai zoba" bayi ta shiga ta sakarwa kanta ruwa tana wankan taji shigowar Janah fitowa tayi suka rungume juna tace "Kaga manyan mata

ke batool kiji tsoron Allah wannan uwar ƙiba da kikayi me kikeci ne a Turain"
Murmushi tayi taci gaba da shafa manta tana gamawa ta zura riga Janah tace “Ba kwanciya zakiyi ba kitse Sarkin bacci tashi zakiyi muje ga motarki can ta rigaki zuwa ki jamu ki kaimu inda angon namu ya ce zamuje gyaran jiki na kwana takwas" kallonta tayi tace “Wai ina kikasan Deen ne Janah?" Dariya tayi sosai tace “Taya bazan san Deen ba bayan kusan koyaushe yana gidannan"
Taɓe baki tayi ta ɗauki wata kanannaɗaɗiyar hula ta ɗora saman sumarta data baje saman bayanta ta yafa mayafin a kafaɗa ta zura takalmi suka fito sai yanzu ta gaisa da danginta da suka cika gidan yan uwan Inna da ƙannen mahaifinta Inna tace “motoci ne guda biyu aka kawosu jiya yace saboda zirga zirgar da zakuyi yanzu key ɗin wacce za'a baki?" Murmushi tayi tace “ki bani na tawa Inna girgiza kai tayi tace “Aa bazaayi haka dani ba Ta Manzo yaba kyauta ai tukuici ki hau tasa don Allah"

Cikin zaƙuwa tace “Shikenan bani key ɗin" remote ɗin Inna ta miƙo mata duka ukun ta fita compound na gidan ta latsa na farko wata hamshaƙiyar mota ta amsa mata ta nufeta gabanta yana faɗuwa ta shiga ta zauna Janah da Samha suka fara baza mata hoto suna mata kirari Janah tace “Wannan amaryar tafi kowacce amarya a shekarar nan Capacity" dariya tayi data sanya kyawawan haƙoranta suka bayyana yar siririyar wushiryarta ta bayyana Janah tayi maza ta baza mata hoto ta shiga motar suka tafi.
Wani katafaren gurin kwalliya da gyaran jikin amare ne me suna MB Bridal Beauty nan Janah tace su tsaya suka tsaya Batul ta tsaya tana ƙarewa wajen kallo iyakar haɗuwa tun daga haraba gurin ya haɗu ta sauke ajiyar zuciya wani sihirtaccen ƙamshi na tashi a gurin, suka taka suka hau saman kamar yanda Janah tace musu, suna shiga taga ma'aikatan suna zubewa suna gaisheta tare da wata irin girmamawa ita dai bata fahimci komai ba ta ɗauka dabi'arsu ce girmama customer.
Wata kyakkyawar mace ce ta fito da ganinta kasan ba tamu bace cikin hausarta da bata fita tace “Barka da zuwa Hajiya mu shiga daga ciki" babu musu sukabi bayanta a parlour tace su Janah su zauna ita kuma suka shiga ciki matar tace “Ranki ya daɗe sunana Nuriyyah Surukarki ita ta bani damar yi Miki gyaran da ba'a taɓa yiwa wata amarya irinsa tace keɗin ta musamman ce" ƙasa tayi da kanta batare da tace komai ba, tun daga wannan lokaci suka fara gyaran jikin wannan amarya taga masifa yanda ake durzar jikinta da haɗin dilka saida tayi kamar tace ta shiga uku ta lalace" iya gyaran na rana ɗaya tayi wani fitinannen kyau da haske, sai yamma Hajiya Nuriyyah take sanar da ita gidanta zasu wucce akwai abubuwan da bazasu yiwu a shagon ba da tayi tunanin zuwa gidansu to kuma aikin baya buƙatar hayaniy.

Saida su Samha suka shiga maganar sannan ta yarda suka tafi can ɗin Jany kam da Jalal a Inna suka barsu a takaice Saida aka ɗauki sati guda ana wannan gyaran jiki ita kanta Batool bata gajiya da kallon kanta tayi wani fitinannen kyau ga wani zaunannen ƙsmshi daya zauna daram a jikinta ko wuccewa tayi sai guri ya haura sama da 1 hour yana ƙamshinta duk wannan abinda akeyi tsakaninta da Deen sai test ko kuma Muhsin yazo ya kawo mata saƙo baya ɗaga

wayarta sosai abin yake ƙular da ita amma ya zatayi da tayi masa complain ma cewa yayi da ita haka al'adarsu take idan biki ya rage saura sati biyu amarya da ango basu ƙara magana sai a gidansu, sannan yace mata tayi haƙuri da duk wani Event susa ayi musu saukar Kur'ani suyi sadaka su taimaki marasa ƙarfi da miskinai yafi su kashe kuɗaɗe a Event.
Matuƙa ta shiga mamaki da wannan sauyin lokaci ɗaya da take fuskanta gurin angon nata Duk yanda taso fahimtar dashi tanada mutane da zasuzo mata waɗanda sukayi zama dasu a Austaralia ya barta tayi Event ko ɗaya ne fir ya nuna rashin amincewarsa yace shi albarkar aurensa yake nema da samun dawamamme zaman lafiya da zuri'a ɗayyiba ranar taci kuka tasha takaici gashi duk wanda ta nemi shawararsa sai yace to ta haƙura mana ai yafita gaskiya.
Haka ta haƙura ranar Event ta zama Ƙur'ani day haka suka shirya cikin wasu manyan hijjabai harda niƙaf sukaje gurin, tabbas Zuciyarta ta gasƙata ba babu bace ta sashi soke mata Event da gaske albarkar aurensa yake nema domin duk wanda yazo sai an haɗa masa complete tea basket madara Milo Nescafe Lipton da Envelope me ɗauke da Dala ɗari da hamsin bayan kyautar ƙur'ani da sallaya da casbaha da hisnul Muslim da kowa yake samu, anci ansha an ƙarya kasusuwan kaji an tauna tsokar raguna, karfe tara taro ya tashi wanda ya zama na farko daya kafa tarihin bam mamaki a birnin Kano.
Suna komawa suka tarar  an kawo kayan lefen da ya tashi kan kowa, goma saura amma dangin amarya da dukkan yan unguwa kowa a tsaye yake cirko cirko saboda al'ajabin wannan lafe iya akwatuna guda ɗari biyu ne banda iyayen akwatunan kaba suma guda hamsin Wasu kalar akwatunan ma tunda Allah ya halicce ta ko a film bata taɓa ganin irinsu ba saboda girmansu da ƙawatuwarsu, Itadai amarya tsoro ne ya kamata na wannan abu me kama da saida rayuwa, zuwa yanzu ta fara dasa ayar tambaya akan Deen ta fara tantama akansa, shi ɗin waye ina yake samun kuɗi in kuma yi masa ake shin iyayen nasa su waye da basajin asarar barnar da kuɗi haka?.........

*Paid book 500 VIP 1k via 9031307566 Fauziyya Tasiu Umar Opay.*

*Contact me*
*09013718241*
[7/11, 11:42 AM] Oum Hairan: *SIGNED MARRIAGE*
*_(Kalma ɗaya)_*

*Oum Hairan*

*___________________________________*
*Book 2 page 23-24*
*___________________________________*

Washegari ta kama ranar juma'a a tsarin bikin ranar yini ce washegari asabar a ɗaura aure hakan ce ta faru sunyi yininsu ba ƙarya ankar uwar kuɗi a kuma ranar ne akayi kamun amarya, ranar amarya taga al'ada su irin nasu kamun ma na masu hannu da shuni daban yake dana yaku bayi a iya dangi ma da sukazo kamu sun haɗa kuɗi bana wasa ba wai kuɗin Lipton nasu na buzaye, suka rinƙa hotuna da amarya wata baturiyar tsohuwa tazo ta rungumeta aka rinƙa kafta musu hoto matasan dangin suna tsokanar tsohuwar suna cewa “Granny ta rungumi kishiyarta Granny tayi mubaya'a" yanda kowa ke nuna mata ƙauna da kulawa a wannan ahli ya tashi kanta batasan sanda ta kama hawaye ba, gsky ta aminta Deen ɗan gata ne babu ƙarya, kowa murna yake tayashi na samunta matsayin iyalinsa duk da cewa kuwa ta samu naƙasu amma babu kyara babu tsangwama haka suke nuna mata soyayya, sunata carafke da Jany da kamar sune suka raɗa mata sunan suna cewa da Granny ga Namesake ɗinta dama sunanta yace zaisa indai aka haifa masa baby girl to gashi ya cika alƙawari, da suka tashi komawa ne Granny tace yace a tafi da Jany ta fara shiga danginta kafin Mom ɗinta ta biyo baya.
Haka aka tafi da Jany yarinyar tanata yima mamanta baybay itadai don anfi ƙarfinta ne but tafison tilon ɗiyarta a jikinta ko yaushe, bayan sun gama bidi'arsu sun tafi ne suma suka fara shirin kwanciya kasancewar dare ya shiga a lokacin ma 11:30pm zare kayan jikinta ta rinƙayi ɗaya bayan ɗaya tana ajiyewa faɗuwar gabanta na nunkuwa ninkin wanda take fuskanta kusan sati biyu kenan, kwanciya tayi a gadon kanta yana kallon sama Zuciyarta na ƙara hargitsewa, tayi nisa sosai a cikin tunani taji wayarta tayi ƙara alamar shigowar saƙo ta ɗauka da sauri zuwa yanzu ta matsu taji daga gareshi.

Ilai kuwa wata baƙuwar number ce ta Turo mata sakon, _"Aysha ta girma Wife ina fatan kin shirya karɓar wani babyn soon ko?"_ Murmushi tayi ta rubuta masa _“Yeah Inason sama mata me ɗaibe mata kewa banso ta taso da kaɗaici kamar Ni"_ Sake turo mata yayi da cewa _"Na matsu naga wannan lokaci Fateemah wlh ji nake kamar ba zan kai goben ba, idan na tuna saura 10 hours ki zama mallakina halal wadda bazan fuskanci ƙalubalen komai a sanda nake gabatar da komai ba ji nake farin ciki yana neman kai numfashina ƙarshe, don Allah ki kula dani Bea....."_ zabura tayi ta tashi zaune ƙirjinta na bada wani dam! dam!  Ta sake kallon saƙon tare da maimaita “Bea! Bea fah?" Maza tayi ta kira layin amma babu amsa tayi kira yakai uku sannan akayi rejected saƙo ya shigo da cewa.
_“Ki daina gaggawa duk abinda kikeson sani zaki sanshi nan da 24 hours kinji_ da haka ya kashe wayar ta koma kiran layin Deen still shima saƙon ne yace mata _“Don Allah Zumata ki kwanta Saida safe banso ki makara wajen tashi da asuba kiyi mana addu'ar shiga rayuwar aure cikin nasara kinji, so nake mu fara da twins Idan mata ne mu samu Fateemah da Sukaina idan maza ne musa musu Nuraddeen da Taheer"_

Komawa tayi ta kwanta tana murmushi tare da yin addu'a ta shafa ta ja duvet ta rufe jikinta Samha dake chat ta kalleta ta kawar da kai, wannan dare baccin Batool rabi da rabi ne iya daɗin bacci idan ta tuna gobe iyanzu tana gidan Deen matsayin matarsa sai tashi tana me riskar kanta da faɗuwar gaba a haka aka cinye daren asubayi tayi sukayi sallah gidan ya kacame da hargowar yan biki wannan ya sasu sulalewa suka tafi gidan maƙota acan sukayi nasu yinin kasancewar ba'a Kano za'a ɗaura auren ba a Y'ar kuka ne yasa basusan meye ya wakana ba ƙarfe biyu na rana ta idar da sallah kenan saƙo ya isheta a waya ta ɗauki wayar da sauri cike da faɗuwar gaba hannunta da dukkannin jikinta yana ɓari, so take ta buɗe saƙon saidai tsoron me zata gani a jiki takeyi itadai tasan yau ita ne ranar ƙarshe kuma tana cikin awanta na ƙarshe matsayin mallakar kanta da mahaifiyarta cikin ƙasa da yan mintina daƙiƙu ko awa take shirin zama mallakar waninta kuma ikonsa lumshe idanunta tayi lokacin da Janah ta karɓi wayar ta buɗe saƙon ta fara karantawa a bayyane _“Alhmdllh! Alhmdllh!! Alhmdllh!!! Fateemah bayan kawo result na gwajin jini da kwayoyin hallitarki da bayyana nawa yau dai burina ya cika na amsa sunan mijinki na sunnah Alhamdulillahi ya rabbil azeezul mannah! Fateemah nayi alƙawarin kare mutumcinki da ƙimarki har fitar numfashina na ƙarshe, na gode Fateemah"_
Zabura tayi ta miƙe jikinta yana ci gaba da rawa hankalinta na ƙara tashi wani irin yanayi na shigarta jiri na ɗibanta abinda ya sabbaba mata zamewa ta zauna tanajin wani baƙon al'amari yana shigarta wanda tunda take bata taɓa fuskanta ba a rayuwarta.

Wani irin zazzaɓi taji ya fara sauko mata ta kwantar da kanta bisa kujera tana furta "hasbunallahu wa ni'imal wakil" daidai lokacin wayarta ta fara Ring ta kai idanunta ga sensor ɗin tare da tura hannunta kamar wadda jijiyoyinta suka daina aiki ta ɗauki wayar ta kara a kunnenta suka sauke ajiyar zuciya tare  ta kuwa rushe da kukan da ita kanta batasan ba meye ba, numfashi ya sake saukewa yace “Me kikewa kuka Fateemah?" Cikin sarƙewar murya tace “Shikenan yanzu Nuraddeen Shikenan?" Ajiyar zuciya yayi yace “Hakane Fateemah Shikenan iya Shikenan ɗin ita zan iya faɗa Miki Ina tayaki murnar samun farin cikin da ya sallama farin cikinsa danke, nayi alƙawarin bazan barki a duhun da kike ciki ba Insha Allahu a yau zaki san komai game dani kuma zaki fahimci komai game dani!"
Numfasawa ya kuma yi sannan yace “Motocin da zasu ɗaukeku zuwa airport suna hanya ku zama cikin shiri Amaryarmu bani Samha Inason magana da ita"
Miƙawa Samha wayar tayi Samha tace “Ango kasha ƙamshi yau kam baki ya buɗe kenan" ajiyar zuciya yayi yace “Samha don Allah karku ɓata lokaci mu daga Niger Sudan muka dawo kuma yau zaku taho yanzu haka motocin ɗaukar amarya sun taho Muhsin shine jagora kamar yanda yayi alƙawari" daga haka ya kashe wayar Samha ta saki baki tana bin wayar da kallo,

yanda taji Muryarsa babu walwala babu wani cikakken farin ciki ya sanyata tafiya tunanin to meye yake faruwa musamman a gaɓar furucinsa na ƙarshe da taji Muryar ta kama rawa, to dake ba huruminta bane haka ta miƙawa Batool wayar tana cewa “Wannan sauye sauye sunyi yawa Janah kinji fah yanzu Bama Abujan zasu zauna ba Sudan za'a tafi da amarya kuma a yau ɗinnan" itadai Batul banda kuka babu abinda takeyi wanda ta kasa gane na meyene, itadai bazatace kukan rabuwa da Inna take yi ba domin dama ba tare suke ba sannan bazatace kukan tunanin haɗuwa da Namiji takeyi ba domin tasan namijin da take tunanin samun samansa a naci abune me wahala sannan ba kukan ƙiyayyar Deen takeyi domin kuwa ita ta zaɓeshi cikin tarin manemanta tace shine gwarzonta domin ya cancanta, sannan Jany ta ma rigata samun gurin zama a gidansa, to kukan me take yi ne ita?.

